Rana tana fitowa daga ɗaya gefen zuwa ɗaya tsallaken; ba abin da zai tsere
daga zafinta. 7 Dokar Yahweh cikakkiya ce, tana wartsakar da rai; shaidar
Yahweh kuwa abar dogara ce, tana ba da hikima ga masu buƙata. 8 Ka'idodin
Yahweh dai-dai suke, tana sa zuciya ta ji daɗi; umarnin Yahweh na da kyau,
yana kawo haske ga idanuwa. 9 Tsoron Yahweh tsabbatacce ne, tabbatacce ne
har abada; dokokin Yahweh gaskiya ne dukkansu dai-dai suke! 10 Suna da
girma da daraja fiye da zinariya, fiye ma da zinariyar da aka tace; sun fi zuma
zaƙi, zuman dake ɗigowa daga saƙarsa. 11 I, ta wurinsu bawanka ya sami
gargaɗi; akwai lada mai girma idan an yi biyayya dasu. 12 Wane ne zai iya
rarrrabe kuskuren kansa? Ka tsabtacce ni daga ɓoyayyun laifuffuka. 13 Ka
tsare bawanka kuma daga zunubai marasa kangado; kada ka bari su yi mulki a
kaina. Sa'an nan ne zan zama kamili, zan kuma zama mara laifi daga
laifuffukana masu yawa. 14 Ka sa maganar baƙina da tunanin zuciyata su zama
abin karɓa a wurinka, Yahweh, dutsena da fansata.

## Psalm 20

1 May Yahweh help you in the day of trouble;
may the name of the God of Jacob protect you
2 and send help from the holy place
to support you from Zion.
3 May he call to mind all your offerings
and accept your burnt sacrifice. Selah
4 May he grant you your heart's desire
and fulfill all your plans.
5 Then we will rejoice in your victory,
and, in the name of our God, we will raise banners.
May Yahweh grant all your petitions.

6 Now I know that Yahweh will rescue his anointed one;
he will answer him from his holy heaven
with the saving strength of his right hand.
7 Some trust in chariots and others in horses,
but we trust in the name of Yahweh our God.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**8** They will be brought down and fall,
but we will rise and stand upright!
**9** Yahweh, rescue the king;
help us when we call.

---

**Zabura 20**

**1** Bari Yahweh ya taimake ka a ranar wahala; bari sunan Allah na Yakubu ya
tsare ka, **2** ya kuma aika taimako daga wuri mai tsarki ya kawo maka tallafi
daga Sihiyona. **3** Bari ya tuna da dukkanbaye-bayenka ya kuma karɓi hadayun
ƙonawarka. Selah **4** Ya biya maka buƙatar zuciyarka, ya kuma cika maka
dukkan shirye-shiryenka. **5** Sai mu yi sowa ta farinciki saboda ka ci nasara, a
cikin sunan Allahnmu, zamu ɗaga tutoci. Yahweh zai biya dukkan roƙe-
roƙenmu. **6** Yanzu dai na sani Yahweh zai ceci zaɓaɓɓensa; zai amsa masa daga
wurinsa mai tsarki a sama da iko a hannun damarsa wanda ya cece shi. **7**
Waɗansu sun dogara ga karusansu wasu kuma ga dawakansu, amma mu muna
kira ga Yahweh Allahnmu. **8** Su zasu yi tuntuɓe har su faɗi ƙasa, amma mu
zamu tashi mu tsaya daram! **9** Yahweh, ka ceci sarki; ka taimake mu sa'ad da
muka yi kira.

---

**Psalm 21**

**1** The king rejoices in your strength, Yahweh!
How greatly he rejoices in the salvation you provide!

**2** You have given him his heart's desire
and have not held back the request of his lips. Selah
**3** For you bring him rich blessings;
you placed on his head a crown of purest gold.
**4** He asked you for life; you gave it to him;
you gave him the length of his days forever and ever.
**5** His glory is great because of your victory;
you have bestowed on him splendor and majesty.
**6** For you grant him lasting blessings;
you make him glad with the joy of your presence.
**7** For the king trusts in Yahweh;
through the covenant faithfulness of the Most High
he will not be moved.

**8** Your hand will seize all your enemies;
your right hand will seize those who hate you.
**9** At the time of your anger,


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

you will burn them up as in a fiery furnace.
Yahweh will consume them in his wrath,
and the fire will devour them.
10 You will destroy their offspring from the earth
and their descendants from among the human race.
11 For they intended evil against you;
they conceived a plot with which they will not succeed!
12 For you will turn them back;
you will draw your bow before them.
13 Be exalted, Yahweh, in your strength;
we will sing and praise your power.

---

**Zabura 21**

1 Sarki na yi farinciki cikin ƙarfinka, Yahweh! Babu iyaka ga farincikinsa daga
cikin ceton da ka tanada! 2 Ka biya masa buƙatar zuciyarsa baka kuma hana
masa roƙon leɓunansa ba. Selah. 3 Gama ka kawo masa albarku masu wadata;
ka sanya bisa kansa kambi na tsabar zinariya. 4 Ya nemi rai daga gare ka; ka
bashi; ka bashi tsawon kwanaki har abada abadin. 5 Darajarsa na da girma
sabili da nasarar ka; ka ɗibiya masa daraja da ɗaukaka. 6 Gama ka bashi
madawwaman albarku; ka sashi jin daɗi da farinciki da ke a gabanka. 7 Gama
sarki yana dogara ga Yahweh; ta wurin alƙawarin amincin Maɗaukaki ba zaya
jijjigu ba. 8 Hannunka zaya kama dukkan maƙiyanka; Hannunka na dama zaya
kama waɗanda suka ƙi ka. 9 A lokacin hasalarka; zaka ƙona su sarai kamar
daga cikin tanderu mai ƙuna. Yahweh zai haɗiye su cikin hasalarsa, kuma
wutar za ta cinye su. 10 Zaka hallakar da zuriyarsu daga ƙasar kuma zuriyarsu
daga cikin 'yan adam. 11 Gama sun shirya yi maka mugunta; sun tsiro da shiri
wanda ba za su iya yin nasara ba! 12 Gama za ka sa su koma da baya; zaka jã
kwarinka a fuskarsu. 13 Ka ɗaukaka, Yahweh, cikin ƙarfin ka; zamu raira waƙa
mu kuma yaɓi ikonka.

---

**Psalm 22**

1 My God, my God, why have you abandoned me?
Why are you so far from saving me
and far from the words of my anguish?
2 My God, I cry out in the daytime, but you do not answer,
and at night I am not silent!

3 Yet you are holy;
you sit as king with the praises of Israel.
4 Our ancestors trusted in you;


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

they trusted in you, and you rescued them.
5 They cried to you and they were rescued.
They trusted in you and were not disappointed.

6 But I am a worm and not a man,
a disgrace to humanity and despised by the people.
7 All those who see me taunt me;
they mock me; they shake their heads at me.
8 They say, "He trusts in Yahweh;
let Yahweh rescue him.
Let him rescue him, for he delights in him."

9 For you brought me from the womb;
you made me trust you when I was on my mother's breasts.
10 I have been thrown on you from the womb;
you are my God since I was in my mother's womb!

11 Do not be far away from me, for trouble is near;
there is no one to help.

12 Many bulls surround me;
strong bulls of Bashan surround me.
13 They open their mouths wide against me
like a roaring lion ripping its victim.
14 I am being poured out like water,
and all my bones are dislocated.
My heart is like wax;
it melts away within my inner parts.
15 My strength has dried up like a piece of pottery;
my tongue sticks to the roof of my mouth.
You have laid me in the dust of death.

16 For dogs have surrounded me;
a company of evildoers has encircled me;
they have pierced my hands and my feet.
17 I can count all my bones.
They look and stare at me.
18 They divide my garments among themselves,
they cast lots for my clothes.

19 Do not be far away, Yahweh;
please hurry to help me, my strength!
20 Rescue my soul from the sword,


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

my only life from the claws of wild dogs.
21 Save me from the lion's mouth;
rescue me from the horns of the wild oxen.

22 I will declare your name to my brothers;
in the midst of the assembly I will praise you.
23 You who fear Yahweh, praise him!
All you descendants of Jacob, honor him!
Stand in awe of him, all you descendants of Israel!
24 For he has not despised or abhorred
the suffering of the afflicted one;
Yahweh has not hidden his face from him;
when the afflicted one cried to him, he heard.

25 My praise will be because of you in the great assembly;
I will fulfill my vows before those who fear him.
26 The oppressed will eat and be satisfied;
those who seek Yahweh will praise him.
May your hearts live forever.

27 All the peoples of the earth will remember and turn to Yahweh;
all the families of the nations will bow down before you.
28 For the kingdom is Yahweh's;
he is the ruler over the nations.

29 All the prosperous people of the earth will feast and will worship;
all those who are descending into the dust will bow before him,
those who cannot preserve their own souls alive.
30 A generation to come will serve him;
they will tell the next generation of the Lord.
31 They will come and tell of his righteousness;
they will tell to a people not yet born what he has done!

---

**Zabura 22**

**1** Allahna, Allahna, me yasa ka yashe ni? Me yasa ka yi nisa daga ƙubutar da ni
kuma kayi nisa daga muryata ta azaba? **2** Allahna, na yi kuka da tsakar rana,
amma baka amsa mani ba, da dare kuma ban yi shuru ba! **3** Amma kai mai
tsarki ne; kana zaman sarki tare da yabon Isra'ila. **4** Iyayenmu sun dogara gare
ka; sun dogara gare ka, ka kuma ƙubutar da su. Sun yi kira gare ka an kuma
ƙuɓutar da su. **5** Sun dogara gare ka basu kuma kunyata ba. **6** Amma ni tsutsa
ne ba mutum ba, abin kunya ga "yan adam da kuma abin raini ga mutane. **7**
Dukkan waɗanda suka ganni suka cakune ni; suka yi mani haibaici; suka kaɗa

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

mani kai. **8** Suka ce, "Ya dogara ga Yahweh; bari Yahweh ya kuɓutar da shi.
Bari ya kuɓutar da shi, gama yana fahariya da shi." **9** Gama ka fito dani daga
mahaifa; ka sa in dogara gare ka a sa'ad da nake shan nono wurin mahaifiyata.
**10** Tun daga mahaifa aka jefo ni gare ka; kai Allahna ne tun daga mahaifar
mahaifiyata! **11** Kada ka yi nisa dani, gama damuwa na kusa; babu wani mai
taimako. **12** Bajimai masu yawa sun kewaye ni; Bajimai masu ƙarfi na Bashan
suna zagaye dani. **13** Sun buɗe bakinsu da girma gãba dani kamar zaki mai ruri
yana yagar abin da ya kama. **14** An kwararo ni kamar ruwa, kuma dukkan
ƙasusuwana sun goce. Zuciyata kamar kitse; ta narke daga cikin cikina. **15**
Karfina ya bushe kaf kamar fasasshiyar tukunya; harshena ya manne sama a
bakina. Ka kwantar da ni a cikin ƙurar mutuwa. **16** Gama karnuka suka zagaye
ni; taron masu aikata mugunta suka kewaye ni; suka huda hannuwana da
ƙafafuna. **17** Zan iya ƙirga ƙasusuwana. Suka duba suka kuma zura mani ido.
**18** Suka rarraba tufafina a tsakaninsu, suka jefa ƙuri'a a bisa kayana. **19** Kada
ka yi nisa, Yahweh; ina roƙon ka kayi sauri domin ka taimake ni, ƙarfina! **20** Ka
kuɓutar da raina daga takobi, raina ɗaya daga hannuwan karnukan daji. **21** Ka
cece ni daga bakin zaki; ka kuɓutar dani daga ƙahonni na shanun daji. **22** Zan
furta sunanka ga 'yan'uwana; a tsakiyar taruwar jama'a zan yabe ka. **23** Ku da
kuke tsoron Yahweh, yabe shi! Dukkan ku zuriyar Yakubu, girmama shi! Ku
tsaya cik cikin tsoronsa, dukkan ku zuriyar Isra'ila! **24** Gama baya rena ko yayi
banza da wahalar ƙuntattu ba; Yahweh baya ɓoye fuskarsa daga gare shi ba; a
lokacin da ƙuntacce yayi kira gare shi, ya ji. **25** Yabona zai zama sabili da kai a
cikin babban taron jama'a; Zan cika wa'adina a gaban waɗanda ke tsoron sa.
**26** Tsanantattu za su ci su ƙoshi; Waɗanda suka nemi Yahweh zasu yabe shi.
Bari zukatanku su rayu har abada. **27** Dukkan mazamnan duniya zasu tuna su
kuma juyo ga Yahweh; dukkan iyalan al'ummai zasu durƙusa a gabanka. **28**
Gama mulki na Yahweh ne; shi yake mulki bisa al'ummai. **29** Dukkan
mawadatan mutanen duniya za su yi buki su kuma yi sujada; dukkan su masu
gangarawa zuwa turɓaya zasu durƙusa a gabansa, su waɗanda baza su iya
adana rayyukansu ba. **30** Tsara mai zuwa zata yi masa hidima; zasu gaya wa
tsara ta gaba game da Ubangiji. **31** Zasu zo su kuma yi magana game da
adalcinsa; zasu faɗi abin da yayi ga mutanen da ba a haife su ba.

---

**Psalm 23**

**1** Yahweh is my shepherd; I will lack nothing.
**2** He makes me to lie down in green pastures;
he leads me beside tranquil water.
**3** He brings back my life;
he guides me along paths that are right

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

for his name's sake.
4 Even though I walk through the darkest valley,
I will fear no harm, for you are with me;
your rod and your staff comfort me.

5 You prepare a table before me in the presence of my enemies;
you have anointed my head with oil;
my cup runs over.
6 Surely goodness and covenant faithfulness will pursue me
all the days of my life;
and I will live in the house of Yahweh
for the length of my days!

---

**Zabura 23**

1 Yahweh makiyayina ne; ba zan rasa komai ba. 2 Yana sa ni in kwanta a cikin
korayen makiyayu; yana bi da ni kurkusa da kwantaccen ruwa. 3 Ya maido da
raina; yana bishe ni ta tafarku madaidaita domin sunansa. 4 Ko da ina tafiya ta
cikin kwari na inuwa mafi duhu, ba zan ji tsoron cutarwa ba tun da kana tare
da ni; sandarka da kerenka na ta'azantar da ni. 5 Ka shirya teburi a gabana a
fuskar maƙiyana; ka shafe kaina da mai; ƙoƙona ya cika har yana zuba. 6
Tabbas nagarta da amintaccen alƙawari zasu bi ni dukkan kwanakin raina; zan
kuma zauna a cikin gidan Yahweh na lokaci mai tsawo sosai!

---

**Psalm 24**

1 The earth is Yahweh's, and its fullness,
the world, and all who live in it.
2 For he has founded it upon the seas
and established it on the rivers.

3 Who will ascend the mountain of Yahweh?
Who will stand in his holy place?
4 He who has clean hands and a pure heart;
who has not lifted up a falsehood,
and has not sworn an oath in order to deceive.

5 He will receive a blessing from Yahweh
and righteousness from the God of his salvation.
6 Such is the generation of those who seek him,
those who seek the face of the God of Jacob. Selah

7 Lift up your heads, you gates;
be lifted up, everlasting doors,


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

so that the King of glory may come in!
8 Who is this King of glory?
Yahweh, strong and mighty;
Yahweh, mighty in battle.
9 Lift up your heads, you gates;
be lifted up, everlasting doors,
so that the King of glory may come in!
10 Who is this King of glory?
Yahweh of hosts,
he is the King of glory. Selah

---

**Zabura 24**

1 Kasa ta Yahweh ce, da dukkan cikarta, duniyar, da dukkan mazauna cikinta. 2
Gama ya gina ta a bisa tekuna ya kuma ƙafa ta a bisa koguna. 3 Wane ne zai
haura tudun Yahweh? Wane ne zai tsaya a cikin wurinsa mai tsarki? 4 Shi
wanda ke da hannuwa masu tsarki da kuma zuciya mai tsabta; wanda baya
faɗar ƙarya, ba ya kuma yin rantsuwa domin yayi yaudara. 5 Zai karɓi albarka
daga wurin Yahweh da kuma adalci daga Allah na cetonsa. 6 Haka ya ke ga
tsarar masu neman sa, masu neman fuskar Allah na Yakubu. Selah 7 Tãda
kanku, ku ƙyamare; ku tashi, madawwaman ƙofofi, domin Sarkin daraja ya
shigo ciki! 8 Wane ne wannan Sarkin daraja? Yahweh, mai ƙarfi da girma;
Yahweh, mai girma cikin yaƙi. 9 Tãda kanku, ku ƙyamare; ku tashi,
madawaman ƙofofi, domin Sarki na daraja ya shigo ciki! 10 Wane ne wannan
Sarkin daraja? Yahweh mai runduna, shi ne Sarkin daraja. Selah

---

**Psalm 25**

1 To you, Yahweh,
I lift up my life!
2 My God, I trust in you.
Do not let me be humiliated;
do not let my enemies rejoice triumphantly over me.
3 May no one who hopes in you be disgraced;
may those who act treacherously without cause be ashamed!

4 Make known to me your ways, Yahweh;
teach me your paths.
5 Guide me into your truth and teach me,
for you are the God of my salvation;
I hope in you all day long.
6 Call to mind, Yahweh, your acts of compassion and of covenant faithfulness;


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

for they have always existed.
7 Do not think about the sins of my youth
or my rebelliousness;
Call me to mind with covenant faithfulness
because of your goodness, Yahweh!

8 Yahweh is good and upright;
therefore he teaches sinners the way.
9 He guides the humble in what is right
and he teaches them his way.
10 All the paths of Yahweh are steadfast love and faithfulness
to those who keep his covenant and his solemn commands.
11 For your name's sake, Yahweh,
pardon my iniquity, for it is great.

12 Who is the man who fears Yahweh?
The Lord will instruct him in the way that he should choose.
13 His life will go along in goodness;
and his descendants will inherit the land.
14 The friendship of Yahweh is for those who honor him,
and he makes his covenant known to them.
15 My eyes are always on Yahweh,
for he will free my feet from the net.

16 Turn toward me and have mercy on me;
for I am alone and afflicted.
17 The troubles of my heart are enlarged;
draw me out from my distress!
18 See my affliction and my toils;
forgive all my sins.
19 See my enemies, for they are many;
they hate me with violent hatred.

20 Protect my life and rescue me;
do not let me be humiliated,
for I take refuge in you!
21 May integrity and uprightness preserve me,
for I hope in you.

22 Rescue Israel, God,
from all of his troubles!

---


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**Zabura 25**

1 A gare ka, Yahweh, na miƙa raina! 2 Allahna, Na dogara gare ka. Kar ka bari
a wulaƙanta ni; kar ka bari maƙiyana suyi farincikin nasara a kaina. 3 Duk
wanda yasa begensa a kan kada shi kunyata bari waɗanda suke aikata makirci
babu dalili su ji kunya! 4 Ka bayyana mani hanyarka, Yahweh; koya mani
tafarkinka. 5 Bishe ni cikin gaskiyarka ka kuma koyar dani, gama kai ne Allah
na cetona; na sa begena bisan ka a koda yaushe. 6 Ka tuna, Yahweh, ayyukanka
na tausayi da kuma amintaccen alƙawari; gama sun kasance tun tuni. 7 Kada
kayi tunanin zunubaina na ƙuruciyata ko tayarwata; ka tuna da ni game da
amintaccen alƙawarinka sabili da alherinka, Yahweh! 8 Yahweh yana da
nagarta kuma yana da alheri saboda haka yana koyawa masu zunubi tafarki. 9
Yana bi da kamili ga abin da ke dai-dai kuma yana koya masu hanyarsa. 10
Dukkan tafarkun Yahweh na dawwamammiyar ƙauna ne da kuma aminci ga
waɗanda ke kiyaye alƙawarinsa da kuma umarnansa tabbatattu. 11 Sabili da
sunanka, Yahweh, ka gafarta zunubina, gama yana da girma sosai. 12 Wane ne
mutumin dake tsoron Yahweh? Ubangiji zaya umarce shi a hanyar da zaya
zaɓa. 13 Rayuwarsa zata bi ta hanya mai kyau; kuma zuriyarsa zasu gaji ƙasar.
14 Abokantakar Yahweh na ga waɗanda ke girmama shi, kuma yana sanar da
alƙawarinsa gare su. 15 Idanuna suna bisa Yahweh koda yaushe, gama zaya
ƙuɓutar da sawayena daga tarko. 16 Ka juyo gare ni kayi mani jinƙai; gama ni
kaɗai ne kuma cikin ƙunci. 17 Damuwoyin zuciyata sun yawaita; ka tsamo ni
daga nawayata! 18 Ka dubi wahalata da kuma matsalolina; ka gafarta
zunubaina. 19 Ka dubi maƙiyana, gama suna da yawa; suna ƙina da ƙiyayya mai
zafi. 20 Ka kare raina ka kuma kuɓutar da ni; kada ka bari a wulaƙanta ni,
gama ina samun mafaka a wurinka! 21 Bari nagarta da aminci su kiyaye ni,
gama begena a cikinka ya ke. 22 Ka kuɓutar da Isra'ila, Allah, daga dukkan
wahalolinsa!

---

**Psalm 26**

1 Judge me, Yahweh,
for I have walked with integrity;
I have trusted in Yahweh without wavering.
2 Examine me, Yahweh, and test me;
test the purity of my inner parts and my heart!
3 For your covenant faithfulness is before my eyes,
and I walk about in your faithfulness.

4 I do not associate with deceitful people,
nor do I mingle with dishonest people.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**5** I hate the assembly of evildoers,
and I do not live with the wicked.
**6** I wash my hands in innocence,
and I go around your altar, Yahweh,
**7** to sing a loud song of praise
and report all your wonderful deeds.

**8** Yahweh, I love the house where you live,
the place where your glory lives!
**9** Do not sweep me away with sinners,
or my life with men of bloodshed,
**10** in whose hands there is a plot,
and whose right hand is full of bribes.

**11** But as for me, I will walk in integrity;
redeem me and have mercy on me.
**12** My foot stands on level ground;
in the assemblies will I bless Yahweh!

---

**Zabura 26**

**1** Yi mani shari'a, Yahweh, gama nayi tafiya da aminci; na dogara ga Yahweh
babu ja da baya. **2** Ka gwada ni, Yahweh, ka kuma jaraba ni; jaraba tsabtar
cikin raina da zuciyata! **3** Gama amintaccen alƙawarinka na gaban idanuna,
kuma ina tafiya cikin amincinka. **4** Ban yi hurɗa da mutane marasa gaskiya ba,
ko in yi cuɗanya da mutane macuta ba. **5** Na ƙi jinin taruwar masu aikata
mugunta, ban kuma zauna da mugaye ba. **6** Na wanke hannuna cikin rashin
laifi, ina kuma zagaya bagadinka, Yahweh, **7** domin in raira waƙar yabo da ƙarfi
in kuma shaida dukkan ayyukanka masu ban girma. **8** Yahweh, ina ƙaunar
gidan da kake zama, inda ɗaukakarka take! **9** Kada ka kawar dani tare da masu
zunubi, ko raina tare da mutane masu marmarin shan jini, **10** waɗanda a cikin
hannuwansu akwai mugun shiri, kuma hanunsa na dama ke cike da rashawa.
**11** Amma ni, zan yi tafiya cikin aminci; ka fanshe ni ka kuma yi mani jinƙai. **12**
Sawayena suna tsaye a shimfiɗarɗiyar ƙasa; a cikin taruwa zan albarkaci
Yahweh!

---

**Psalm 27**

**1** Yahweh is my light and my salvation;
whom should I fear?
Yahweh is my life's refuge;
whom should I dread?


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

2 When evildoers approached me to devour my flesh,
my adversaries and my enemies stumbled and fell.
3 Though an army encamps against me,
my heart will not fear;
though war rises up against me,
even then I will remain confident.

4 One thing have I asked of Yahweh,
and I will seek that:
that I may live in the house of Yahweh
all the days of my life,
to see the beauty of Yahweh
and to meditate in his temple.
5 For in the day of trouble
he will hide me in his shelter;
in the cover of his tent he will conceal me.
He will lift me high on a rock!

6 Then my head will be lifted up above my enemies all around me,
and I will offer sacrifices of joy in his tent!
I will sing and make songs to Yahweh!

7 Hear, Yahweh, my voice when I cry out!
Have mercy on me, and answer me!
8 My heart says about you,
"Seek his face!" I seek your face, Yahweh!
9 Do not hide your face from me;
do not turn your servant away in anger!
You have been my helper;
do not abandon me or reject me,
God of my salvation!
10 Even if my father and my mother abandon me,
Yahweh will take me in.

11 Teach me your way, Yahweh!
Lead me on a level path
because of my enemies.
12 Do not give me up to the desires of my enemies,
for false witnesses have risen up against me,
and they breathe out violence!

13 What would have happened to me
if I had not believed that I would see the goodness of Yahweh
in the land of the living?

**14** Wait for Yahweh;
be strong, and let your heart be courageous!
Wait for Yahweh!

---

**Zabura 27**

**1** Yahweh ne haske na da cetona; wane ne zan ji tsoro? Yahweh ne mafakar
raina; wane ne zai razana ni? **2** Lokacin da masu aikata mugunta suka taso
mani domin su cinye namana, magabtana da maƙiyana suka yi tuntuɓe suka
kuma faɗi. **3** Koda runduna zasu zagaye ni da gãba, zuciyata baza ta ji tsoro ba;
koda yaƙi zai taso gãba dani, duk da haka zan kasance da ƙarfin hali. **4** Abu
guda ɗaya nayi roƙo ga Yahweh, zan kuma biɗi wannan; shi ne in zauna a cikin
gidan Yahweh dukkan kwanakin raina, in dubi kyawun Yahweh in kuma yi
bimbini a cikin haikalinsa. **5** Gama a ranar wahala zaya ɓoye ni a cikin
fukafukansa; a ƙarƙashin inuwar rumfarsa zaya suturce ni. Zaya ɗaukaka ni a
bisa dutse mai tsawo! **6** Sa'an nan za a ɗaukaka kaina fiye da maƙiyana dake
kewaye dani, zan kuma miƙa hadayu na farinciki a cikin rumfarsa! Zan raira
waƙa in kuma yi waƙoƙi ga Yahweh! **7** Yahweh ka ji, muryata a lokacin da nayi
kuka! Kayi mani jinƙai, ka kuma amsa mani! **8** Zuciyata na ce da kai, "Nemi
fuskarsa!" Na nemi fuskarka, Yahweh! **9** Kada ka ɓoye fuskarka daga gare ni;
kada ka juyar da bawanka daga gare ka cikin fushi! Tun dama kaine mai
taimakona; kada ka yashe ni ko kayi banza dani, Allah na cetona! **10** Koda
mahaifina ko mahaifiyata sun yashe ni, Yahweh zaya karɓeni. **11** Ka koya mani
tafarkinka, Yahweh! Ka bishe ni a daidaitacciyar hanya saboda maƙiyana. **12**
Kada ka bayar da ni ga nufin maƙiyana, gama shaidun ƙarya sun tashi gãba
dani, suna kuma huro da ta'addanci! **13** Da mene ne zai faru dani da ba domin
na yarda cewa zan ga alherin Yahweh a cikin ƙasar masu rai ba? **14** Ka jira ga
Yahweh; yi ƙarfi, bari zuciyarka ta ƙarfafa! Saurari Yahweh!

---

**Psalm 28**

**1** To you, Yahweh, I cry out;
my rock, do not ignore me.
If you do not respond to me,
I will join those who go down to the pit.
**2** Hear the sound of my pleading
when I call for help from you,
when I lift up my hands
toward your most holy place!

**3** Do not drag me away with the wicked,
those who behave wickedly,
who speak peace with their neighbors

but have evil in their hearts.
4 Give them what their deeds deserve
and repay them what their wickedness demands;
repay them for the work of their hands
and render to them their due.

5 Because they do not understand the deeds of Yahweh
or the work of his hands,
he will break them down
and never rebuild them.

6 Blessed be Yahweh
because he has heard the sound of my pleading!
7 Yahweh is my strength and my shield;
my heart trusts in him, and I am helped.
Therefore my heart greatly rejoices,
and I will praise him with singing.

8 Yahweh is the strength of his people,
and he is the saving refuge of his anointed one.
9 Save your people and bless your inheritance.
Be their shepherd and carry them forever.

---

**Zabura 28**

1 A gare ka, Yahweh, nayi kuka; dutsena, kada kayi banza da ni. Idan baka
amsa mani ba, zan harɗe da waɗanda ke gangarawa zuwa kabari. 2 Kaji ƙarar
roƙona a lokacin da nayi kira domin taimako daga gare ka, a lokacin da na tãda
hannuwa na zuwa wurinka mai tsarki! 3 Kada ka kawar dani tare da masu
aikata mugunta, su masu aikata laifuffuka, su dake faɗin alheri da
maƙwabtansu da baki amma zuciyarsu cike take da mugunta. 4 Ka basu dai-dai
abin da ayyukansu ya dace dasu da kuma abin da muguntarsu ta wajaba, ka
biya su bisa ga aikin hannuwansu ka kuma mayar masu bisa ga ladarsu. 5
Domin basu gane da ayyukan Yahweh ba ko ayyukan hannuwansa, zaya buga
su ƙasa baza a ƙara gina su ba. 6 Albarka ga Yahweh domin ya ji muryar
kukana! 7 Yahweh ne ƙarfina da garkuwata; zuciyata ta dogara gare shi, na
kuma sami taimako. Saboda haka zuciyata tayi farinciki ƙwarai, zan kuma yabe
shi da raira waƙoƙi. 8 Yahweh ne karfin mutanensa, kuma shi ne maɓoyar ceto
na shafaffensa. 9 Ka ceci mutanenka ka kuma albarkaci gãdonka. Ka zama
makiyayinsu ka kuma ɗauke su har abada.

---

**Psalm 29**

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

[1] Ascribe to Yahweh, you sons of God,
ascribe to Yahweh glory and strength!
[2] Ascribe to Yahweh the glory his name deserves.
Bow down to Yahweh in the splendor of holiness!

[3] The voice of Yahweh is heard over the waters;
the God of glory thunders,
Yahweh thunders over many waters.
[4] The voice of Yahweh is powerful;
the voice of Yahweh is majestic.
[5] The voice of Yahweh breaks the cedars;
Yahweh breaks in pieces the cedars of Lebanon.
[6] He makes Lebanon skip like a calf
and Sirion like a young ox.
[7] The voice of Yahweh sends out flames of fire.
[8] The voice of Yahweh shakes the wilderness;
Yahweh shakes the wilderness of Kadesh.
[9] The voice of Yahweh causes the oaks to twist
and strips the forests bare.
Everyone in his temple says, "Glory!"

[10] Yahweh sits as king over the flood;
Yahweh sits as king forever.
[11] Yahweh gives strength to his people;
Yahweh blesses his people with peace.

---

**Zabura 29**

[1] Bada yabo ga Yahweh, ku 'ya'yan Allah! Bada yabo ga Yahweh domin
ɗaukakarsa da ƙarfinsa. [2] Ba Yahweh ɗaukakar da ta cancanci sunansa.
Durƙusa ƙasa ga Yahweh cikin jamalin tsarkinsa. [3] An ji muryar Yahweh har
bisa ruwaye; Allah maɗaukaki ya yi tsawa, Yahweh na tsawa bisa ruwaye masu
yawa. [4] Muryar Yahweh na da cikakken iko; Muryar Yahweh mai daraja ne. [5]
Muryar Yahweh na fasa itatuwan sida; Yahweh na fasa gutsu-gutsu itatuwan
sida na Lebanon. [6] Yana sa Lebanon tayi tsalle kamar ɗan maraki da kuma
Dutsen Hamon kamar ɗan shanu. [7] Muryar Yahweh na aikar da harshen wuta.
[8] Muryar Yahweh na girgiza hamada; Yahweh na girgiza hamadar Kadesh. [9]
Muryar Yahweh nasa rimaye su tanƙware tana kuma kware daji a fili. Kowanne
a cikin haikali na cewa, "Daukaka!" [10] Yahweh na zaman sarki a bisa ruwa mai
ambaliya; Yahweh na zaman sarki har abada. [11] Yahweh yana bada karfi ga
mutanensa; Yahweh yana albarkatar mutanensa da salama.

---

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**Psalm 30**

1 I will exalt you, Yahweh,
for you have raised me up
and have not allowed my enemies to rejoice over me.
2 Yahweh my God, I cried to you for help,
and you healed me.
3 Yahweh, you have brought up my soul from Sheol;
you have kept me alive from going down to the pit.

4 Sing praises to Yahweh, you his faithful ones!
Give thanks when you remember his holiness.
5 For his anger is only for a moment;
but his favor is for a lifetime.
Weeping comes for a night,
but joy comes in the morning.

6 In confidence I said, "I will never be shaken."
7 Yahweh, by your favor
you established me as a strong mountain;
but when you hid your face,
I was troubled.

8 I cried to you, Yahweh,
and sought favor from my Lord!
9 What advantage is there in my blood,
if I go down to the grave?
Will the dust praise you?
Will it declare your trustworthiness?
10 Hear, Yahweh, and have mercy on me!
Yahweh, be my helper.

11 You have turned my mourning into dancing;
you have removed my sackcloth and clothed me with gladness.
12 So now my glory will sing praise to you and not be silent;
Yahweh my God, I will give thanks to you forever!

---

**Zabura 30**

1 Zan girmama ka, Yahweh, gama ka tã dani sama kuma baka bari maƙiyana
sun yi farinciki bisa na ba. 2 Yahweh Allahna, nayi kuka gare ka domin taimako,
ka kuma warkar dani. 3 Yahweh, ka tsamo raina daga Lahira; ka adana ni da rai
kada in gangara ƙasa zuwa kabari. 4 Raira yabbai ga Yahweh, ku amintattunsa!


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

Ku bada godiya a lokacin da kuka tuna da tsarkinsa. 5 Gama fushin sa na lokaci
kaɗan ne; amma tagomashinsa na har abada ne. Kuka na zuwa da dare ne,
amma farinciki na zuwa da safe. 6 Da ƙarfin hali nace. "Ba zan jijjigu ba." 7
Yahweh, da tagomashinka ka kafa ni kamar ƙaƙƙarfan tsauni; amma daka ɓoye
fuskarka, na shiga damuwa. 8 Nayi kira gare ka, na kuma nemi tagomashi daga
wurin Ubangijina! 9 Wacce riba ce ke cikin mutuwata, idan na gangara cikin
kabari? Ko turɓaya zata yabe ka? Zata furta tabbatattun amincinka? 10 Ka
saurara, Yahweh, kayi mani jinƙai! Yahweh, ka zama mai taimakona. 11 Ka
juyar da makokina zuwa rawa; ka cire mani tsumma ka kuma sanya mani rigar
farinciki. 12 Yanzu ɗaukakata zata yi maka waƙar yabo kuma ba zata yi shuru
ba; Yahweh Allahna, zan yi maka godiya har abada!

---

**Psalm 31**

1 In you, Yahweh, I take refuge;
never let me be humiliated.
Rescue me in your righteousness.
2 Listen to me; rescue me quickly;
be my rock of refuge,
a stronghold to save me.

3 For you are my rock and my fortress;
therefore for your name's sake, lead and guide me.
4 Pluck me out of the net that they have hidden for me,
for you are my refuge.
5 Into your hands I entrust my spirit;
you will redeem me, Yahweh, God of trustworthiness.

6 I hate those who serve worthless idols,
but I trust in Yahweh.
7 I will be glad and rejoice in your covenant faithfulness,
for you saw my affliction;
you knew the distress of my soul.
8 You have not given me into the hand of my enemy.
You have set my feet in a wide open place.

9 Have mercy upon me, Yahweh, for I am in distress;
my eyes grow weary with grief
with my soul and my body.
10 For my life is weary with sorrow
and my years with groaning.
My strength fails because of my iniquity,
and my bones are wasting away.

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

11 Because of all my enemies, I have become contemptible;
my neighbors are appalled at my situation,
and those who know me are horrified.
Those who see me in the street run from me.
12 I am forgotten as a dead man whom no one thinks about.
I am like a broken pot.
13 For I have heard the whispering of many,
terrifying news from every side
as they plot together against me.
They plot to take away my life.

14 But I trust in you, Yahweh;
I say, "You are my God."
15 My times are in your hand.
Rescue me from the hands of my enemies
and from those who pursue me.
16 Make your face shine on your servant;
save me in your covenant faithfulness.
17 Do not let me be humiliated, Yahweh;
for I call out to you!
May the wicked be humiliated!
May they be silent in Sheol.
18 May lying lips be silenced
that speak against the righteous defiantly
with arrogance and contempt.

19 How great is your goodness
that you have stored up for those who revere you,
that you perform for those who take refuge in you
before all the children of mankind!
20 In the shelter of your presence, you hide them from the plots of men.
You hide them in a shelter from the strife of tongues.

21 Blessed be Yahweh,
for he showed me his marvelous covenant faithfulness when I was in a besieged city.
22 Though I said in my alarm,
"I am cut off from your eyes,"
yet you heard my plea for help
when I cried to you.

23 Love Yahweh, all you faithful ones.
Yahweh protects the faithful,
but he pays back the arrogant in full.

24 Be strong and let your heart take courage,
all you who trust in Yahweh for help.

---

**Zabura 31**

1 A cikin ka, Yahweh, na sami mafaka; kada ka barni in wulaƙanta. Ka kuɓutar
dani cikin adalcinka. 2 Ka saurare ni; Ka kuɓutar dani da sauri; ka zama dutsen
mafakata, ƙaƙƙarfar maɓoya domin cetona. 3 Gama kai ne dutsena da kuma
mafakata; Saboda haka sabili da sunanka, ka shugabance ni ka kuma bishe ni.
4 Ka ƙwato ni daga cikin tãrun da suka ɓoye domi na, gama kai ne maɓuyata. 5
A cikin hannuwanka nake bada ruhuna; zaka fanshe ni, Yahweh, Allah
madogarata. 6 Na ƙi jinin waɗandɑ suke bautawa gumakan banza, amma na
dogara ga Yahweh. 7 Zan yi murna da kuma farinciki cikin amintaccen
alƙawarinka, gama ka ga ƙuncina; ka san matsalar raina. 8 Baka miƙa ni a cikin
hannuwan maƙiyana ba. Ka kafa ƙafafuwana a buɗaɗɗen wuri mai faɗi. 9 Kayi
mani jinƙai, Yahweh, gama ina cikin ƙunci; idanuna sun yi nauyi da azaba tare
da raina da jikina. 10 Gama raina yayi nauyi da makoki kuma shekaruna na
cike da nishe-nishe. Karfina ya gaza sabili da zunubina, ƙasusuwana suna
lalacewa sarai. 11 Sabili da maƙiyana, mutane sun yi banza dani; maƙwabtana
suka gaji da yanayina, kuma waɗanda suka san ni suka tsorata. Waɗanda suka
gamu dani a hanya suka gudu daga gare ni. 12 An manta da ni kamar mataccen
mutum wanda babu wanda ke tunaninsa. Ina kama da fasasshiyar tukunya. 13
Gama na ji raɗe-raɗe masu yawa, labarai masu ban tsoro daga kowanne sashe
sa'ad da suke shiri gãba da ni. Sun yi shiri domin su ɗauke raina. 14 Amma na
dogara gare ka, Yahweh; Na ce, "Kai ne Allahna." 15 Ƙaddarata na cikin
hannuwanka. Ka kuɓutar dani daga hannuwan magabtana daga kuma waɗanda
suke fafarata. 16 Bari fuskarka ta haskaka bisa bawanka; ka cece ni cikin
amintaccen alƙawarinka. 17 Kada ka bar ni in wulaƙantu, Yahweh; gama na yi
kira gare ka! Bari mugu ya wulaƙanta! Bari suyi shuru a cikin Lahira. 18 Bari
harsuna masu ƙarya suyi shuru su dake magana gãba da mai adalci da renin
girma da kuma tozartarwa. 19 girman alherinka da ka shirya wa masu girmama
ka, abin da kake aiwatar wa domin waɗanda suka yi mafaka a cikinka a gaban
dukkan 'ya'yan talikai! 20 A cikin mahallin bayyanuwarka, ka ɓoye su daga
makircin mutane. Ka ɓoye su a cikin mahalli daga ta'addancin harsuna. 21 Mai
albarka ne Yahweh, gama ya nuna mani amintaccen alƙawarinsa mai ban
mamaki a lokacin da nake a cikin birnin kwanto. 22 Ko da ya ke na faɗa cikin
gaggawata, "An datse ni daga fuskarka," duk da haka ka ji roƙona domin
taimako lokacin da nayi kuka gare ka. 23 Oh, ƙaunaci Yahweh, dukkan ku
amintattun mabiya. Yahweh yana tsare amintattu, amma yana sãka wa masu
girman kai. 24 Ku ƙarfafa kuyi ƙarfi, dukkan ku dake dogara cikin Yahweh
domin taimako.

## Psalm 32

**1** Blessed is the person
whose transgression is forgiven,
whose sin is covered.
**2** Blessed is the man to whom Yahweh reckons no guilt
and in whose spirit there is no deceit.

**3** When I remained silent,
my bones were wasting away
while I groaned all day long.
**4** For day and night your hand was heavy upon me.
My strength withered as in summer drought. Selah

**5** Then I acknowledged my sin to you,
and I no longer hid my iniquity.
I said, "I will confess my transgressions to Yahweh,"
and you forgave the guilt of my sin. Selah

**6** For this reason every one of your faithful followers should pray to you
at a time of great distress.
When the surging waters overflow,
the waters will not reach them.
**7** You are my hiding place;
you will guard me from trouble.
You will surround me with the songs of victory. Selah

**8** I will instruct you and teach you in the way which you should go.
I will counsel you with my eye upon you.
**9** Do not be like a horse or like a mule,
which have no understanding;
it is only with bridle and bit to control them
that they will go where you want them to.
**10** The wicked have many sorrows,
but Yahweh's covenant faithfulness will surround the one who trusts in him.
**11** Be glad in Yahweh, and rejoice, you righteous;
shout for joy, all you who are upright in heart.

## Zabura 32

**1** Mai albarka ne taliki wanda an gafarta masa kurakuransa, wanda aka rufe
zunubinsa. **2** Mai albarka ne mutum wanda Yahweh ba ya lisafta laifi bisansa

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

kuma wanda babu algus cikin ruhunsa. 3 Da na yi shuru, ƙasusuwana suna
lalacewa sa'ad da nake nishe-nishe dukkan yini. 4 Gama rana da dare
hannunka na da nauyi bisana. ƙarfina ya gaza kamar lokacin fãrin kaka. 5 Sa'an
nan na furta zunubi na gare ka, ban kuma ƙara ɓoye laifi na ba. Na ce, "Zan
furta kurakuraina ga Yahweh," ka kuma gafarta mani ladar zunubina. 6 Saboda
wannan, dukkan waɗanda ke na allahntaka suna adu'a a gare ka a lokacin
gwagwarmaya mai girma. Sa'an nan lokacin da ruwaye masu hauka suka taso,
baza su cimma waɗannan mutane ba. 7 Kai ne maɓuyata; zaka tsare ni daga
wahala. Zaka zagaye ni da waƙoƙin nasara. 8 Zan umarce ka in koya maka
hanyar da zaka bi. Zan umarce ka da idanuna a bisanka. 9 Kada ka zama kamar
doki ko kamar alfadari, wanda ba shi da fahimta; sai tare da linzami da ragama
domin a bi da su inda ake so su tafi. 10 Mugu yana da baƙinciki mai yawa,
amma amintaccen alƙawarin Yahweh zai zagaye wanda ya dogara gare shi. 11
Yi murna cikin Yahweh, da farinciki, ku adalai; yi sowa ta farinciki, dukkan ku
masu tsabta cikin zuciya.

---

**Psalm 33**

1 Rejoice in Yahweh, you righteous;
praise is appropriate for the upright.
2 Give thanks to Yahweh with the harp;
sing praises to him with the lute having ten strings.
3 Sing to him a new song;
play skillfully and shout for joy.

4 For Yahweh's word is upright,
and all his deeds are done in faithfulness.
5 He loves righteousness and justice.
The earth is full of Yahweh's covenant faithfulness.

6 By the word of Yahweh the heavens were made,
and all the stars were made by the breath of his mouth.
7 He gathers the waters of the sea together like a heap;
he puts the oceans in storehouses.
8 Let the whole earth fear Yahweh;
let all the inhabitants of the world stand in awe of him.
9 For he spoke, and it was done;
he commanded, and it stood in place.

10 Yahweh frustrates the alliances of nations;
he overrules the plans of the peoples.
11 The plans of Yahweh stand forever,


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

the plans of his heart for all generations.

12 Blessed is the nation whose God is Yahweh,
the people whom he has chosen as his own inheritance.
13 Yahweh looks from heaven;
he sees all the people.
14 From the place where he lives,
he looks down on all who live on the earth.
15 He who shapes the hearts of them all
observes all their deeds.

16 No king is saved by a vast army;
a warrior is not saved by his great strength.
17 A horse is a false hope for victory;
in spite of his great strength, he cannot rescue.
18 See, Yahweh's eye is on those who fear him,
on those who hope in his covenant faithfulness
19 to deliver their lives from death
and to keep them alive in times of famine.

20 We wait for Yahweh;
he is our help and our shield.
21 Our hearts rejoice in him,
for we trust in his holy name.
22 Let your covenant faithfulness, Yahweh, be with us
as we put our hope in you.

---

**Zabura 33**
1 Yi farinciki cikin Yahweh, ku adalai; Yin yabo ya dace ga adalai. 2 Kuyi godiya
ga Yahweh da molo; yi waƙoƙin yabo gare shi da molo mai tsarkiya goma. 3
Raira sabuwar waƙa gare shi; ku yi kiɗa da ƙwarewarku kuna raira waƙa tare
da farinciki. 4 Gama maganar Yahweh mai adalci ce, kuma dukkan abin da ya
aikata dai-dai ne. 5 Yana ƙaunar adalci da shari'a. Duniya na cike da
amintaccen alƙawarinsa. 6 Da maganar Yahweh aka hallici sammai, kuma
dukkan taurari sun kasance ne ta numfashin bakinsa. 7 Yana tara ruwayen teku
wuri ɗaya kamar tudu; ya ajiye tekuna cikin ɗakunan ajiya. 8 Bari dukkan
ƙasar taji tsoron Yahweh; Bari dukkan mazaunan duniya su tsaya cik a
gabansa. 9 Gama ya yi magana, aka kuma aikata; ya umarta, ya kuma tabbata.
10 Yahweh yana lalatar da ƙawancen al'ummai; yana mulki akan shirye-shiryen
mutane. 11 Shirin Yahweh ya tsaya har abada, shirye-shiryen zuciyarsa ga
dukkan tsararraki. 12 Mai albarka ce al'ummar da Yahweh ne Allahnta,

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

mutanen da ya zaɓa abin gãdonsa. 13 Yahweh yana gani daga sama; yana ganin
dukkan mutane. 14 Daga wurin da ya ke zama, yana duban dukkan masu zama
cikin ƙasar. 15 Shi wanda ya ke shirya zuciyarsu dukka yana la'akari da
ayyukansu. 16 Babu sarkin da zai tsira sabili da yawan runduna; jarumi baya
tsira ta dalilin ƙarfinsa. 17 Doki tsaro ne na banza domin nasara; duk da
ƙarfinsa, ba zai iya ƙubutarwa ba. 18 Duba, idanun Yahweh na bisan waɗanda
ke tsoronsa, a bisa waɗanda suka dangana bisa amintaccen alƙawarinsa 19
domin ya kuɓutar da rayukansu daga mutuwa ya kuma kiyaye su da rai a
lokacin yunwa. 20 Muna jiran Yahweh; shi ne taimakonmu da kuma
garkuwarmu. 21 Zuciyarmu tayi farinciki cikinsa, gama mun dogara cikin
sunansa mai tsarki. 22 Bari amintaccen alƙawarinka, Yahweh, ya kasance da
mu a lokacin da muka kafa begenmu cikinka.

---

**Psalm 34**

**1** I will praise Yahweh at all times,
his praise will always be in my mouth.
**2** I will praise Yahweh!
May the oppressed hear and rejoice.
**3** Praise Yahweh with me,
let us lift up his name together.

**4** I sought Yahweh and he answered me,
and he gave me victory over all my fears.
**5** Those who look to him are radiant,
and their faces are not ashamed.
**6** This oppressed man cried and Yahweh heard him
and saved him from all his troubles.
**7** The angel of Yahweh camps around those who fear him
and rescues them.

**8** Taste and see that Yahweh is good.
Blessed is the man who takes refuge in him.
**9** Fear Yahweh, you his holy people.
There is no lack for those who fear him.
**10** The young lions sometimes lack food and suffer hunger,
but those who seek Yahweh will not lack anything good.
**11** Come, sons, listen to me.
I will teach you the fear of Yahweh.
**12** What man is there who delights in life
and loves many days,
that he may see good?


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

13 Then keep your tongue from evil
and keep your lips from speaking lies.
14 Turn away from evil and do good.
Seek peace and go after it.

15 The eyes of Yahweh are on the righteous
and his ears are directed toward their cry.
16 The face of Yahweh is against those who do evil,
to cut off the memory of them from the earth.

17 The righteous cry out and Yahweh hears
and he rescues them from all their troubles.
18 Yahweh is close to the brokenhearted,
and he saves those who are crushed in spirit.

19 Many are the troubles of the righteous,
but Yahweh delivers them out of them all.
20 He keeps all his bones,
not one of them will be broken.

21 Evil will kill the wicked.
Those who hate the righteous will be condemned.
22 Yahweh rescues the lives of his servants.
None of those who take refuge in him will be condemned.

---

**Zabura 34**

1 Zan yabi Yahweh a dukkan lokaci, Yabonsa zai kasance a bakina koda yaushe.
2 Zan yabi Yahweh! Bari ƙuntattu su ji su kuma yi farinciki. 3 Ku yabi Yahweh
tare da ni, bari mu ɗaukaka sunansa tare. 4 Na nemi Yahweh kuma ya amsa
mani, ya kuma ba ni nasara bisa dukkan tsorona. 5 Waɗanda ke duban sa suna
haskakawa, kuma fuskarsu ba ta ji kunya ba. 6 Wannan matsattsen mutum yayi
kuka Yahweh kuma ya ji ya kuma cece shi daga dukkan matsalolinsa. 7
Mala'ikan Yahweh na zagaye waɗanda ke tsoronsa ya kuma ƙubutar da su. 8 Ku
ɗanɗana ku kuma gani cewa Yahweh na da kyau. Mai albarka ne mutum wanda
ke ɓuya cikinsa. 9 Ku ji tsoron Yahweh, ku mutanensa masu tsarki. Babu rashi
ga waɗanda ke tsoronsa. 10 'Ya'yan zakuna wasu lokuttan suna rasa abinci su
kuma ji yunwa, amma waɗanda suka nemi Yahweh baza su rasa kowanne abu
mai kyau ba. 11 Ku zo, 'ya'ya maza, ku saurare ni. Zan koya maku jin tsoron
Yahweh. 12 Wanne mutum ne mai biɗar rai ya ke kuma ƙaunar ranaku masu
yawa, domin ya ga alheri? 13 To, sai ka tsare harshenka daga faɗin mugunta

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

leɓunanka kuma daga faɗin ƙarya. 14 Ka juyo daga barin mugunta ka kuma
aikata nagarta. Nemi salama ka kuma bi ta. 15 Idanun Yahweh suna bisa masu
adalci kuma kunnuwansa suna karkatawa zuwa ga kukansu. 16 Fuskar Yahweh
na gãba da waɗanda ke aikata mugunta, domin a datse tunawa da su daga
duniya. 17 Masu adalci sun yi kira Yahweh kuma yana kuɓutar da su daga
dukkan matsalolinsu. 18 Yahweh yana kurkusa da masu karyayyar zuciya, kuma
yana ceton waɗanda aka ƙuntatawa a cikin ruhu. 19 Da yawa suke matsalolin
masu adalci, amma Yahweh yana ƙubutar da su daga dukkan su. 20 Ya kare
dukkan ƙasusuwansa, babu ko ɗaya daga cikinsu da za a karya. 21 Mugunta
zata kashe mai mugunta. Waɗanda suka ƙi masu adalci za a hallakar da su. 22
Yahweh yana ƙubutar da rayukan bayinsa. Babu ɗaya daga cikin waɗanda ke
neman mafaka wurinsa da za a kayar.

---

**Psalm 35**

**1** Yahweh, work against those who work against me;
fight against those who fight against me.
**2** Grab your small shield and large shield;
rise up and help me.
**3** Use your spear and battle ax
against those who chase me;
say to my soul,
"I am your salvation."

**4** May those who seek my life
be shamed and dishonored.
May those who plan to harm me
be turned back and ashamed.
**5** May they be as chaff before the wind,
as the angel of Yahweh drives them away.
**6** May their way be dark and slippery,
as the angel of Yahweh chases them.

**7** Without cause they set their net for me;
without cause they dug a pit for my life.
**8** Let destruction overtake them by surprise.
Let the net that they have set catch them.
Let them fall into it, to their destruction.
**9** But I will be joyful in Yahweh
and rejoice in his salvation.
**10** All my bones will say,
"Yahweh, who is like you,

who rescues the oppressed from those who are too strong for them
and the poor and needy from those who try to rob them?"

11 Unrighteous witnesses rise up;
they accuse me falsely.
12 They repay me evil for good.
I am sorrowful.
13 As for me, when they were sick, my clothing was sackcloth;
I fasted for them,
and my prayer returned to my bosom.
14 I went about in grief as for my brother;
I bent down in mourning as for my mother.
15 But when I stumbled, they rejoiced and gathered together;
they gathered together against me, and I was surprised by them.
They tore at me without stopping.
16 With no respect at all they mocked me;
they grind their teeth at me in rage.

17 Lord, how long will you look on?
Rescue my soul from their destructive attacks,
my only life from the lions.
18 Then I will thank you in the great assembly;
I will praise you among many people.
19 Do not let my deceitful enemies rejoice over me;
do not let them carry out their wicked schemes.
20 For they do not speak peace,
but they devise deceitful words
against those in our land who live in peace.
21 They open their mouths wide against me;
they said, "Aha, Aha, our eyes have seen it."

22 You have seen it, Yahweh, do not be silent;
Lord, do not be far from me.
23 Arouse yourself and awake to my defense;
My God and my Lord, defend my cause.
24 Defend me, Yahweh my God, because of your righteousness;
do not let them rejoice over me.
25 Do not let them say in their heart, "Aha, we have what we wanted."
Do not let them say, "We have devoured him."

26 May they be put to shame and may they be humiliated who rejoice at my distress.
May those who exalt themselves over me be clothed with shame and

dishonor.

**27** Let those who desire my vindication
shout for joy and be glad;
may they say continually, "Yahweh be praised,
he who delights in the welfare of his servant."

**28** Then I will tell of your justice
and praise you all day long.

---

**Zabura 35**

**1** Yahweh, ka yi gãba da waɗanda ke aiki gãba da ni; ka yaƙi waɗanda ke yaƙi
da ni. **2** Ka ɗauki garkuwarka ƙarama da babba; tashi ka taimake ni. **3** Yi
amfani da mashi da gatarin yaƙin ka gãba da waɗanda ke runtuma ta; ka ce da
raina, "Ni ne cetonka." **4** Bari su waɗanda ke neman raina su ji kunya su kuma
faɗi. Bari waɗanda ke shirin cuta na a juyar da su a kuma hargitsa su. **5** Bari su
zama kamar ƙaiƙayi a fuskar isaka, a sa'ad da mala'ikan Yahweh ke korar su. **6**
Bari hanyar su ta duhunta tana kuma zamewa, a sa'ad da mala'ikan Yahweh ke
runtumar su. **7** Babu dalili suka shirya mani tarkonsu; Babu dalili suka haƙa
rami domin raina. **8** Bari halakarwa ta auko masu ba zato. Bari tarkon da suka
ɗana ya kama su. Bari su faɗa ciki, ga hallakarsu. **9** Amma zan yi farinciki cikin
Yahweh in kuma yi murna cikin cetonsa. **10** Dukkan ƙasusuwana za su ce,
"Yahweh, wane ne kamar ka, wanda ke ƙuɓutar da ƙuntattu daga waɗanda
suka fi ƙarfinsu da kuma matalauta da kuma mabuƙata daga waɗanda ke
ƙoƙarin yi masu fashi?" **11** Shaidu marasa adalci sun tashi; sun yi mani zargin
ƙarya. **12** Sun sãka mani nagarta da mugunta. Ina cike da ɓacin rai. **13** Amma a
lokacin da suke ciwo, na sanya tsummokara; na yi azumi a madadinsu da kaina
sunkuye ga ƙirjina. **14** Na yi tafiya cikin ƙunci domin ɗan'uwana; Na durƙusa
cikin makoki domin mahaifiyata. **15** Amma da nayi tuntuɓe, suka yi murna suka
taru wuri ɗaya; suka taru wuri ɗaya gãba da ni, kuma suka bani mamaki. Suka
kawo mani farmaƙi babu fasawa. **16** Da rashin girmamawa samsam suka yi
mani ba'a; suka tauna mani haƙoransu. **17** Ubangiji, har yaushe zaka duba? Ka
ƙuɓutar da raina daga farmaƙinsu mai hallakarwa, raina daga zakuna. **18** Sa'an
nan zan gode maka a babban taro mai girma; Zan yabe ka a cikin mutane masu
yawa. **19** Kada ka bar maƙiyana masu ƙarya su yi murna a kaina; kada ka barsu
su aiwatar da mugun shirinsu. **20** Gama basu maganar salama, amma suka
shirya maganganun ƙarya gãba da waɗanda ke zaman salama cikin ƙasar. **21**
Sun buɗe bakunansu da girma gãba da ni; suka ce, "Aha, Aha, idanunmu sun
gan shi." **22** Ka gan shi, Yahweh, kada ka yi shuru; Ubangiji, kada kayi nisa
dani. **23** Ka tãda kanka ka kuma farka domin ka kare ni; Allahna da Ubangijina,
ka kare bukatata. **24** Ka kãre ni, Yahweh Allahna, sabili da adalcinka; kada ka
bar su suyi murna a kaina. **25** Kada ka bari su faɗa a cikin zuciyarsu, Aha, mun


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

sami abin da muke nema." Kada ka bar su su ce, "Mun haɗiye shi." 26 Ka basu
kunya ka kuma ruɗar da waɗanda ke niyyar cutar da ni. Bari waɗanda ke
cakuna ta a rufe su da kunya da ƙasƙanci. 27 Bari su dake marmarin kuɓutata
suyi sowa ta murna su kuma ji daɗi; bari koyaushe su ce, "Bari Yahweh ya
ɗaukaka, shi da ya ke jin daɗi cikin wadatar bawansa." 28 Sa'an nan zan faɗi
game da shari'arka in kuma yabe ka dukkan yini.

---

**Psalm 36**

1 An evil man speaks of his transgression from deep in his heart,
there is no fear of God in his eyes.

2 For he comforts himself,
thinking that his iniquity will not be discovered and be hated.
3 The words of his mouth are wickedness and deceit;
he does not want to be wise and do good.
4 While he lies in bed, he plans ways to sin;
he sets out on an evil way;
he does not reject evil.

5 Your covenant faithfulness, Yahweh, reaches to the heavens;
your faithfulness reaches to the clouds.
6 Your righteousness is like the mountains of God;
your judgments are like the great deep.
Yahweh, you preserve both mankind and the animals.
7 How precious is your covenant faithfulness, God!
Humanity takes refuge under the shadow of your wings.
8 They feast upon the abundance of your house;
you let them drink from the river of your delights.
9 For with you is the fountain of life;
in your light we will see light.

10 Extend your covenant faithfulness fully to those who know you,
your defense to the upright of heart.
11 Do not let the foot of the arrogant man come near to me.
Do not let the hand of the wicked drive me away.
12 Over there those who behave wickedly have fallen;
they have been pushed down and are not able to get up.

---

**Zabura 36**

1 Mugun mutum yana zancen kurakuransa daga cikin zuciyarsa, babu tsoron
Allah a idanunsa. 2 Gama yana yiwa kansa ta'aziya, da tunanin cewar

 

zunubansa ba zasu tonu ba ko kuma a ƙi su. 3 Maganganunsa na zunubi ne da
yaudara; ba ya son ya zama mai hikima ya kuma aikata nagarta. 4 A lokacin da
ya ke kwance a gado, yana shirya yadda zai yi zunubi; ba ya ƙin mugunta. 5
Amintaccen alƙawarinka, Yahweh, na kaiwa har zuwa sammai; amincinka na
kaiwa zuwa cikin giza-gizai. 6 Adalcinka na kama da duwatsun Allah;
shari'unka na kama da manyan zurfafa. Yahweh, ka kare talikai da dabbobi. 7
Yaya darajar amintaccen alƙawarinka ya ke, Allah! Bil'adama na fakewa a
ƙarƙashin inuwar fukafukanka. 8 Zasu ƙoshi daga yalwar abincin gidanka; zaka
sa su sha daga cikin koginka mai manyan albarku. 9 Domin a gare ka akwai
maɓulɓular rai; cikin haskenka zamu ga haske. 10 Ka kawo gare ni amintaccen
alƙawarinka cikakke ga waɗanda suka san ka, kariyarka zuwa ga kamilai a
zuci. 11 Ka da ka bar ƙafafun mai girman kai shi zo kusa dani. Ka da ka bar
hannun mugaye su kore ni da nisa. 12 A can mugaye suka faɗi; aka buga su
ƙasa basu kuma iya tashi ba.

---

**Psalm 37**

1 Do not be irritated because of evildoers;
do not be envious of those who act unrighteously.
2 For they will soon dry up as the grass
and wither as the green plants.

3 Trust in Yahweh and do what is good;
settle in the land and graze in faithfulness.
4 Then delight yourself in Yahweh,
and he will give you the desires of your heart.

5 Give your ways to Yahweh;
trust in him, and he will act on your behalf.
6 He will display your justice like the daylight
and your innocence like the day at noon.

7 Be still before Yahweh
and wait patiently for him.
Do not be angry if someone succeeds in what he does,
or when he makes evil plots.

8 Do not be angry and frustrated.
Do not worry. This only makes trouble.
9 Evildoers will be cut off,
but those who wait for Yahweh will inherit the land.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

10 In a little while the evil man will disappear;
you will look at his place, but he will be gone.
11 But the meek will inherit the land
and will delight in great prosperity.

12 The wicked man plots against the righteous
and he grinds his teeth in rage against him.
13 The Lord laughs at him,
for he sees that his day is coming.

14 The wicked have drawn out their swords
and have bent their bows
to cast down the oppressed and needy,
to kill those who are upright.
15 Their swords will pierce their own hearts,
and their bows will be broken.

16 Better is the little that the righteous has
than the abundance of many wicked people.
17 For the arms of the wicked people will be broken,
but Yahweh supports the righteous people.

18 Yahweh watches over the blameless day by day,
and their heritage will be forever.
19 They will not be ashamed when times are bad.
When famine comes, they will have enough to eat.

20 But evil men will perish.
Yahweh's enemies will be like the splendor of the pastures;
they will be consumed and disappear in the smoke.

21 The wicked person borrows but does not repay,
but the righteous person is generous and gives.
22 Those who are blessed by God will inherit the land;
those who are cursed by him will be cut off.

23 It is by Yahweh that a man's steps are established,
the man whose way is commendable in God's sight.
24 Though he stumbles, he will not fall down,
for Yahweh is holding him with his hand.

25 I was young and now am old;
I have never seen the righteous person abandoned

or his children begging for bread.
26 All the day long he is gracious and lends,
and his children become a blessing.

27 Turn away from evil and do what is right;
then you will be safe forever.
28 For Yahweh loves justice
and does not abandon his faithful ones.
They are preserved forever,
but the descendants of the wicked will be cut off.
29 The righteous will inherit the land
and live there forever.

30 The mouth of the righteous person speaks wisdom
and increases justice.
31 The law of his God is in his heart;
his feet will not slip.

32 The wicked person spies on the righteous person
and seeks to kill him.
33 Yahweh will not abandon him into the evil person's hand
or condemn him when he is judged.

34 Wait for Yahweh and keep his way,
and he will raise you up to possess the land.
You will see when the wicked are cut off.

35 I have seen the wicked and terrifying person
spread out like a green tree in its native soil.
36 But when I passed by again, he was not there.
I looked for him, but he could not be found.

37 Observe the man of integrity, and mark the upright;
there is a good future for a man of peace.
38 Rebels will be totally destroyed;
the future for the wicked man is cut off.

39 Salvation of the righteous comes from Yahweh;
he is their place of safety in the times of trouble.
40 Yahweh helps them and rescues them.
He rescues them from evil men and saves them
because they have taken refuge in him.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

## Zabura 37

**1** Kada ka damu da masu mugunta; kada ka ji ƙyashin waɗanda ke ayyukan
rashin adalci. **2** Gama zasu bushe da wuri kamar ciyawa, su kuma yanƙwane
kamar korayen tsire-tsire. **3** Ka dogara ga Yahweh kuma ka yi abin da ke
nagari; ka zauna a ƙasar ka yi kiwo cikin aminci. **4** Sa'an nan ka yi murna da
al'amuran Yahweh, kuma zai biya maka buƙatun zuciyarka. **5** Ka miƙa
hanyoyinka ga Yahweh; ka dagara gare shi, kuma zai yi abu a madadinka. **6** Zai
nuna aɗalcinka kamar hasken rana da rashin laifinka kamar rana tsaka. **7** Ka
natsu a gaban Yahweh kuma kayi jira da haƙuri domin sa. Kada ka ji haushi
idan wani ya yi nasara da abin da ya ke yi, ko sa'ad da ya ke ƙulla mugunta. **8**
Kada ka ji haushi da takaici. Kada ka damu. Wannan na bada damuwa ne
kawai. **9** Za a datse miyagu, amma waɗanda ke jiran Yahweh zasu gãji ƙasar. **10**
A ɗan lokaci ƙaɗan mugun mutum zai ɓace; zaka dubi wurinsa, amma ba zai
kasance ba. **11** Amma masu tawali'u zasu gãji ƙasar kuma zasu yi murna da
gagarumar wadata. **12** Mugun mutum yana shirya maƙarƙashiya gãba da adali
yana kuma cizon haƙora gãba da shi. **13** Ubangiji yana yi masa dariya, gama
yana ganin zuwan ranarsa. **14** Mugaye sun zare takubbansu suka kuma
tanƙware bakkunansu don su kãda waɗanda ake masu danniya da masu
buƙata, su kashe waɗanda ke da nagarta. **15** Takkubansu zasu soke zukatansu,
kuma bakkunansu zasu kakkarye. **16** Gara ƙanƙanen abin da mutumin kirki ya
ke da shi da yawan abubuwan mugayen mutane. **17** Gama za a ƙarɓe ƙarfin
mugayen mutane, amma Yahweh zai taimaki adalai **18** Yahweh yana lura da
marasa abin zargi a kowacce rana, kuma gãdonsu zai kasance har abada. **19** Ba
za su ji kunya a lokacin masifa ba. Sa'ad da Yunwa tazo, zasu samu isasshen
abinci. **20** Amma mugaye zasu lalace. Maƙiyan Yahweh za su zama kamar
darajar ciyawa; za a cinye su su ɓace kamar hayaƙi. **21** Mugu yakan ci bashi
amma ba ya biya, amma adali yana bayarwa hannu sake. **22** Waɗanda Allah ya
sawa albarka zasu gãji ƙasar; waɗanda ya la'anta zasu zama korarru. **23** Ta
wurin Yahweh ne hanyoyin mutum ke kafuwa, mutumin da hanyarsa
amintacciya ce a fuskar Allah. **24** Ko da ya ke yana tuntuɓe, ba zai faɗi ba,
gama Yahweh na riƙe shi da hannunsa. **25** Dã ni yaro ne kuma yanzu na tsufa;
ban taɓa ganin an yashe da adali ba ko kuma 'ya'yansa na roƙon abinci. **26**
Dukkan yini yana yin alheri yana ba da rance, kuma 'ya'yansa sun zama
albarka. **27** Ka bar mugunta kayi abin da ke dai-dai; zaka cetu har abada. **28**
Gama Yahweh yana ƙaunar adalci kuma baya rabuwa da amintattun masu
binsa. Yana kiyaye su har abada, amma zuriyar mugaye zasu zama korarru. **29**
Adalai zasu gãji ƙasar su zauna ciki har abada. **30** Bakin adali yana maganar
hikima da kuma ƙara adalci. **31** Shari'ar Allahnsa na zuciyarsa; ƙafafunsa ba za


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

su yi santsi ba. 32 Mugu yakan yi fakon adali ya nemi hanyar kashe shi. 33
Yahweh ba zai bar shi a hannun mugun ba ko kuwa ya yanke masa hukunci
sa'ad da ya ke masa shari'a. 34 Ka jira Yahweh ka kuma kiyaye hanyoyinsa,
zaya kuma ɗaga ka sama ka mallaki ƙasar. Za ka gani sa'ad da ake korar
mugaye. 35 Na ga mugu da azzalumin taliki ya baje kamar koren itace a
ƙasarsa ta asali. 36 Amma sa'ad da na sãke wucewa kuma, bai kasance a wurin
ba. Na neme shi, amma ba ya samuwa. 37 Dubi mutumin kirki, ka kuma lura da
adali; gaba zai zama da kyau ga mutumin salama, 38 Masu zunubi kuwa za a
hallaka su ƙaƙaf; za a kuma share zuriyar mugun mutum. 39 Ceton adalai
yakan zo daga Yahweh ne; yakan kiyaye su a lokatan damuwa. 40 Yahwe ya
taimake su ya kuɓutar da su, Ya kuɓutar dasu daga mugaye ya cece su saboda
sun sami garkuwa a cikinsa.

---

**Psalm 38**

1 Yahweh, do not rebuke me in your anger;
    do not punish me in your wrath.
2 For your arrows pierce me,
    and your hand presses me down.
3 There is no soundness in my body because of your anger;
    there is no health in my bones because of my sin.
4 For my iniquities overwhelm me;
    they are a burden too heavy for me.

5 My wounds are infected and smell
    because of my foolish sins.
6 I am stooped over and humiliated every day;
    I go about mourning all day long.
7 For within me, I am filled with burning;
    there is no health in my flesh.
8 I am numb and utterly crushed;
    I groan because of the anguish of my heart.

9 Lord, you understand my heart's deepest yearnings,
    and my groanings are not hidden from you.
10 My heart pounds, my strength fades,
    and the light of my eyes, even that is not with me.
11 My friends and companions shun me because of my condition;
    my neighbors stand far off.
12 Those who seek my life lay snares for me.
    They who seek my harm speak destructive words
    and say deceitful words all day long.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**13** But I, I am like a deaf man and hear nothing;
I am like a mute man who says nothing.
**14** I am like a man who does not hear
and who has no reply.
**15** Surely I wait for you, Yahweh;
you will answer, Lord my God.
**16** I say this so that my enemies will not rejoice over me.
If my foot slips, they will do terrible things to me.

**17** For I am about to stumble,
and I am in constant pain.
**18** I confess my guilt;
I am anxious about my sin.
**19** But my enemies are numerous;
those who hate me wrongfully are many.
**20** They repay me evil for good;
they hurl accusations at me
although I have pursued what is good.

**21** Do not abandon me, Yahweh;
my God, do not stay far away from me.
**22** Come quickly to help me,
Lord, my salvation.

---

**Zabura 38**

**1** Yahweh, kada ka tsauta mani a cikin fushinka; kada ka hukunta ni a cikin
hasalarka. **2** Gama kibiyoyinka suna sukana, kuma hannunka na matse ni har
ƙasa. **3** Dukkan jikina na ciwo saboda hasalarka; babu lafiya a ƙasusuwana
saboda laifina. **4** Gama zunubaina sun fi ƙarfina; sun zamar mani kaya mai
nauyi da yawa. **5** Raunukana sun harbu suna wari saboda wawancin zunubaina.
**6** Ana dakatar dani ana wulaƙanta ni kowacce rana; Ina ta makoki dukkan
tsawon rana. **7** Gama daga ciki, ina cike da zafin ciwo; babu lafiya a jikina. **8** An
sandare ni an ragargaza ni; ina gunaguni saboda fushin zuciyata. **9** Ubangiji
kana sane da buƙatar zuciyata, kuma gunagunina basa ɓoyu ba daga gare ka.
**10** Zuciyata na bugawa, ƙarfina na ƙarewa, bana kuma gani sosai. **11** Abokaina
da aminai sun ƙaurace mani saboda yanayina; maƙwabtana na tsaye daga nesa.
**12** Waɗanda ke so su kashe ni sun ƙafa mani tarko. Su waɗanda ke neman yi
mani rauni suna maganar hallakarwa da faɗin kalmomin ruɗu dukkan tsawon
rana. **13** Amma ni, ina kamar kurman mutum kuma bana jin komai; ina kamar
beben da ba ya iya faɗin komai. **14** Ina kamar mutumin da ba ya ji kuma ba shi


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

da amsa. 15 Tabbas ina jiranka, Yahweh; zaka amsa, Ubangiji, Allahna. 16 Na
faɗi haka saboda maƙiyana ba zasu yi murna a kan damuwata ba. Idan tafin
ƙafata ya zame, zasu yi mani mugayen abubuwa. 17 Gama ina gab da mutuwa,
kuma ina cikin wahala kowacce sa'a. 18 Na furta laifofina; na kuma damu da
zunubina. 19 Amma maƙiyana na da yawa; waɗanda suka ƙi ni cikin kuskure na
da yawa. 20 Suna rama mani nagarta da mugunta; suna ta tuhuma ta koda ya
ke ina neman abin da ke nagari. 21 Kada ka yashe ni, Yahweh; Allahna, kada ka
tsaya nesa dani. 22 Ka zo da sauri ka taimakeni, Ubangiji, cetona.

---

**Psalm 39**

**1** I decided, "I will watch what I say
so that I do not sin with my tongue.
I will muzzle my mouth
while in the presence of an evil man."
**2** I kept silent;
I kept back my words even from saying anything good,
and my pain grew worse.
**3** My heart became hot;
when I thought about these things,
it burned like a fire.
Then finally I spoke.

**4** "Yahweh, make me know when will be the end of my life
and the extent of my days.
Show me how transient I am.
**5** See, you have made my days only the width of my hand,
and my lifetime is like nothing before you.
Surely every man is a single breath. Selah

**6** Surely every man walks about like a shadow.
Surely everyone hurries about
to accumulate riches although they do not know who will receive them.

**7** Now, Lord, for what am I waiting?
You are my only hope.
**8** Rescue me from my sins;
do not make me the scorn of fools.
**9** I am silent and cannot open my mouth,
because it is you who has done it.
**10** Stop wounding me;
I am overwhelmed by the blow of your hand.
**11** When you discipline people for iniquity,


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

you consume the things they desire like a moth;
surely all people are nothing but vapor. Selah

12 Hear my prayer, Yahweh,
and give ear to my cry for help;
do not be deaf to my tears!
for I am like a foreigner with you,
a sojourner like all my ancestors were.
13 Turn your gaze from me so that I may smile again
before I die."

---

**Zabura 39**

1 Na yi shiri, "Zan lura da furcin da zan yi saboda kada in yi zunubi da harshe
na. Zan sa wa bakina takunkumi a lokacin da nake wurin da mugu ya kasance."
2 Na yi shiru; Na riƙe maganganuna daga faɗin wani abu koda nagari ne,
shanwuta kuma ta ƙaru. 3 Zuciyata ta yi zafi; sa'ad da nayi tunani a kan
abubuwan nan, yana ci kamar wuta. Sa'an nan a ƙarshe nayi magana. 4
"Yahweh, kasa in san yaushe ne ƙarshen rayuwata da tsawon kwanakina. Ka
nuna mani ina kurkusa da matuwa. 5 Duba, kã maida kwanakina kamar tsawon
hannuna, kuma rayuwata kamar ba komai take ba a wurinka. Hakika kowanne
mutum lumfashi ɗaya ne. Selah 6 Hakika kowanne mutum yana tafiya kamar
inuwa. Hakika dukkan kowa yana hanzari ya tattara arziki ko da yake basu san
wanda zai karbe su ba. 7 Yanzu, Ubangiji, domin me nake jira? Kai ƙaɗai ne
begena. 8 Ka cece ni daga zunubaina; kada ka bari in zama abin ba'a ga
wawaye. 9 Na yi shiru kuma bazan iya buɗe bakina ba, saboda kai ne kayi
haka. 10 Ka daina yi mani rauni; na karaya ta wurin bugun hannunka. 11 Sa'ad
da kake horar da mutane don zunubi, kakan cinye abubuwan da suke marmari
kamar asu; hakika dukkan mutane ba komai bane banda tururi kawai. Seleh 12
Ka ji addu'ata, Yahweh, ka saurare ni; ka saurari kukana! Kada ka zama kurma
a gare ni, gama ni kamar baƙo ne tare da kai, ɗan gudun hijira kamar yadda
dukkan kakannina suke. 13 Ka juyar da hararrarka daga gare ni domin in sake
yin murmushi kafin in mutu,"

---

**Psalm 40**

1 I waited patiently for Yahweh;
he listened to me and heard my cry.
2 He brought me up out of a horrible pit,
out of the miry clay,
and he set my feet on a rock
and made my steps secure.
3 He has put a new song in my mouth,


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

praise to our God.
Many will see it and honor him
and will trust in Yahweh.

4 Blessed is the man
who makes Yahweh his trust
and does not honor the proud
or those who turn away from him to lies.
5 Many, Yahweh my God,
are the wonderful deeds that you have done,
and your thoughts which are about us cannot be numbered;
if I declared and spoke of them,
they would be more than could be counted.

6 You have no delight in sacrifice or offering,
but you have opened my ears;
you have not required burnt offerings or sin offerings.
7 Then said I, "See, I have come;
it is written about me in the scroll of the document.
8 I delight to do your will, my God;
your laws are in my heart."

9 I have proclaimed good news of your righteousness in the great assembly;
Yahweh, you know that my lips have not kept back from doing this.
10 I have not concealed your righteousness in my heart;
I have declared your faithfulness and your salvation;
I have not concealed your covenant faithfulness
or your trustworthiness from the great assembly.

11 Do not keep back your acts of mercy from me, Yahweh;
let your covenant faithfulness and your trustworthiness always preserve me.
12 Troubles that cannot be numbered surround me;
my iniquities have caught up with me so that I am no longer able to see anything;
they are more than the hairs on my head,
and my heart has failed me.
13 Be pleased, Yahweh, to rescue me;
hurry to help me, Yahweh.

14 Let them be ashamed and completely disappointed
who pursue my life to sweep it away.
Let them be turned back and brought to dishonor,
those who delight in hurting me.
15 Let them be appalled because of their shame,


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

those who say to me, "Aha, aha!"
16 But may all those who seek you rejoice
and be glad in you;
let everyone who loves your salvation say continually,
"May Yahweh be praised."

17 I am poor and needy;
yet the Lord thinks about me.
You are my help and you come to my rescue;
do not delay, my God.

---

**Zabura 40**

1 Na jira Yahweh da haƙuri; ya saurare ni ya ji kukana. 2 Ya fitar dani daga
rami mai furgitarwa, daga taɓo, ya sa ƙafafuna a kan dutse ya tsare takawata.
3 Ya sa sabuwar waƙa a bakina, yabo ga Allahnmu. Da yawa zasu gani su kuma
girmama shi su dogara ga Yahweh. 4 Mai albarka ne mutumin da ya maida
Yahweh madogararsa kuma baya girmama masu fahariya ko waɗanda suka
juya daga gare shi zuwa ƙarairayi. 5 Da yawa suke, Yahweh Allahna, ayyukan
al'ajiban da ka yi, kuma babu wanda zai iya ƙirga abubuwan da kake tunani
gme da mu; Idan na yanke shawara in yi magana a kan su, za su fi abin da za a
iya ƙirgawa. 6 Ba ka buƙatar hadaya ko baiko, amma ka buɗe kunnuwana; ba
ka buƙatar baye-baye na ƙonawa ko baye-baye na zunubi. 7 Sa'an nan na ce,
"Duba, Na zo; a rubuce ya ke a game dani cikin littafin Yahweh. 8 Ina jin daɗin
yin nufinka, Allahna, shari'unka na cikin zuciyata." 9 Na yi shelar nagartattun
labaran ayyukanka na adalci a babban taron jama'a; Yahweh, ka san leɓunana
basu dena yin wannan ba. 10 Ban ɓoye ayyukan adalcinka a zuciyata kaɗai ba;
Na furta amincinka da cetonka; Ban ɓoye amintaccen alƙawarinka ko
madawwamiyar ƙaunarka daga babban taron jama'a ba. 11 Kada ka yi jinkirin
yi mani ayyukan jinƙai; ka bar amintaccen alƙawarinka da madawwamiyar
ƙaunarka su kiyaye ni. 12 Damuwoyin da basu ƙidayuwa sun kewaye ni; alhakin
zunubaina ya tarar da ni har yasa bana iya ganin wani abu; Sun fi gashin kaina
yawa, kuma zuciyata ta karaya. 13 In ka yarda, Yahweh, ka cece ni; ka yi
hanzari ka taimake ni, Yahweh. 14 Ka sa waɗanda suke son kashe ni su sha
kunya da yawa. Kasa su koma baya a ci nasara a kansu, ka kawo waɗanda ke
murna saboda wahalar da nake sha, cikin ƙasƙanci. 15 Kasa su razana saboda
kunya, su waɗanda ke yi mani ba'a, " 16 Amma bari dukkan waɗanda ke neman
ka su yi farinciki da murna a cikinka; ka sa duk mai ƙaunar cetonka ya ci gaba
da cewa, "A yabi Yahweh." 17 Na talauce na zama mabuƙaci; duk da haka
Ubangiji yana tunani a kai na. Kai ne mai taimako na kuma ka zo domin ka cece
ni; kada ka yi jinkiri, Allahna.

---


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**Psalm 41**

1 Blessed is he who is concerned for the weak;
in the day of trouble, Yahweh will rescue him.
2 Yahweh will preserve him and keep him alive,
and he will be blessed on the earth;
Yahweh will not turn him over to the will of his enemies.
3 Yahweh will support him on the bed of suffering;
you will make his bed of sickness into a bed of healing.

4 I said, "Yahweh, have mercy on me!
Heal me, for I have sinned against you."
5 My enemies speak evil against me, saying,
'When will he die and his name perish?'
6 If my enemy comes to see me,
he says worthless things;
his heart gathers up wickedness for itself;
when he goes away from me, he tells others about it.

7 All who hate me whisper together against me;
against me they hope for my hurt.
8 They say, "An evil disease holds on tightly to him;
now that he is lying down, he will rise up no more."
9 Indeed, even my own close friend, in whom I trusted,
who ate my bread,
has lifted up his heel against me.

10 But you, Yahweh, have mercy on me and raise me up
so that I may pay them back.
11 By this I know that you delight in me,
for my enemy does not triumph over me.
12 As for me, you support me in my integrity
and will keep me before your face forever.

13 May Yahweh, the God of Israel be praised
from everlasting to everlasting.
Amen and Amen.

---

**Zabura 41**

1 Mai albarka ne wanda ke kulawa da marasa ƙarfi; a ranar masifa, Yahweh zai
'yantar da shi. 2 Yahweh zai kiyaye shi ya kare shi, kuma zai zama da albarka a
duniya; Yahweh ba zai bar shi ga nufin maƙiyansa ba. 3 Yahweh zai yi masa


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

gudummawa a gadon wahalarsa; zaka maida gadonsa na ciwo zuwa gadonsa na
warkarwa. 4 Na ce, "Yahweh, ka yi mani jinƙai! Ka warkar dani, gama na yi
maka laifi." 5 Maƙiyana suna muguwar magana gãba da ni, cewa, 'Yaushe ne
zai mutu kuma sunansa ya lalace?' 6 Idan maƙiyina ya zo gani na, ya furta
maganganun banza; zuciyarsa na ƙoƙarin sanin dukkan matsalolina; sa'ad da
ya tafi daga gare ni, sai ya gaya wa kowa game da su. 7 Dukkan waɗanda ke ƙi
na na raɗa da juna gãba da ni; gãba da ni suna fatan shan wahalata. 8 Suna
cewa, "Mugun ciwo ya make shi; yanzu da ya ke kwance ƙasa, ba zai ƙara tashi
ba." 9 Lallai, ko abokina na ƙut da ƙut, da na yarda da shi, wanda ya ci
gurasata, ya juya mani baya. 10 Amma kai, Yahweh, ka yi mani jinƙai ka ɗaga
ni sama saboda in mai da martani. 11 Ta wannan na san kana farinciki dani,
gama maƙiyina bai yi murna a kaina ba. 12 Amma ni, ka tallefe ni cikin
aminncina kuma zaka kiyaye ni a fuskarka har abada. 13 Bari Yahweh, Allah na
Isra'ila a yabe shi daga dawwama zuwa dawwama. Amin da Amin. Littafi Biyu

---

**Psalm 42**

1 As the deer pants after streams of water,
so I thirst for you, God.
2 I thirst for God, for the living God,
when will I come and appear before God?
3 My tears have been my food
day and night,
while my enemies are always saying to me,
"Where is your God?"
4 These things I call to mind
as I pour out my soul:
how I went with the throng
and led them to the house of God
with the voice of joy and praise,
a multitude celebrating a festival.

5 Why are you bowed down, my soul?
Why are you upset within me?
Hope in God,
for again I will praise him who is my salvation.

6 My God, my soul is bowed down within me,
therefore I call you to mind from the land of the Jordan,
from the three peaks of Mount Hermon, and from the hill of Mizar.
7 Deep calls to deep at the noise of your waterfalls;
all your waves and your billows have gone over me.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**8** Yet Yahweh will command his covenant faithfulness in the daytime;
in the night his song will be with me,
a prayer to the God of my life.

**9** I will say to God, my rock,
"Why have you forgotten me?
Why do I go mourning
because of the oppression of the enemy?"
**10** As with a sword in my bones, my adversaries rebuke me,
while they always say to me, "Where is your God?"

**11** Why are you bowed down, my soul?
Why are you upset within me?
Hope in God,
for again I will praise him who is my salvation and my God.

---

**Zabura 42**

**1** Kamar yadda mariri ke marmarin rafukan ruwa, haka nake ƙishinka, Allah. **2**
Ina ƙishin Allah, Allah mai rai, yaushe zan zo in bayyana a gaban Allah? **3**
Hawayena sun zama abincina dare da rana, lokacin da maƙiyana kullum suna
cewa dani, "Ina Allahnka?" **4** Waɗannan abubuwan nake tunawa da su yayin da
nake zubo raina: yadda na tafi tare da taron mutane na jagorance su zuwa
gidan Allah tare da muryar jin daɗi da yabo, babban taro na shagalin buki. **5**
Me yasa ka rusuna ƙasa, raina? Me yasa kake damuwa daga can ciki? Yi bege
ga Allah, gama zan ƙara yabonsa wanda shi ne cetona. **6** Allahna, raina ya
rusuna ƙasa a can ciki, don haka na tuna da kai daga ƙasar Yordan, daga
ƙololuwar Dutsen Hamon, kuma daga tudun Miza. **7** Zurfi na kira ga zurfi da jin
ƙarar kwararowar ruwanka; dukkan raƙuman ruwanka da matsirgan ruwanka
sun mamaye ni. **8** Duk da haka Yahweh zai umarci amintaccen alƙawarinsa da
rana; da dare waƙarsa zata kasance tare da ni, addu'a ce ga Allah na rayuwata.
**9** Zan yi magana ga Allah, dutsena, "Me yasa ka mance da ni" Me yasa nake
makoki saboda danniyar maƙiyina?" **10** Kamar da takobi a ƙasusuwana,
maƙiyana ke yi mani zargi, yayin da kullum suke cewa dani, "Ina Allahnka?" **11**
Me yasa kake rusuna a ƙasa, raina? Me yasa kake damuwa can ciki? Yi bege
cikin Allah, gama kuma zan yabe shi wanda shi ne cetona da Allahna.

---

**Psalm 43**

**1** Bring me justice, God,
and plead my case against a nation that is not faithful.
Deliver me from the deceitful and unjust man.
**2** For you are the God of my strength.

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

Why have you rejected me?
Why do I go about in mourning
because of the oppression of the enemy?
3 Oh, send out your light and your truth,
let them lead me.
Let them bring me to your holy hill
and to your dwelling.
4 Then I will go to the altar of God,
to God my exceeding joy.
I will praise you with the harp,
God, my God.

5 Why are you bowed down, my soul?
Why are you upset within me?
Hope in God,
for again I will praise him who is my salvation and my God.

---

**Zabura 43**
1 Kawo mani adalci, Allah, kayi mani taimakon kãriya a kan al'umma marasa
tsoron ka. 2 Gama kai ne Allah na ƙarfina. Meyasa ka yashe ni? Me yasa nake
tafiya cikin makoki saboda muzgunawar maƙiya? 3 Oh, ka aiko da haskenka da
gaskiyarka, su jagorance ni. su kawo ni ga tudunka mai tsarki da wurin
zamanka. 4 Sa'an nan zan yi tafya zuwa ga bagadin Allah, ga Allah matuƙar jin
daɗina. Zan yabeka da garaya, Allah, Allahna. 5 Me yasa ka rusuna ƙasa, raina?
Me ya sa kake damuwa can ciki? Yi bege cikin Allah, gama zan ƙara yabonsa
wanda shi ne cetona da Allahna.

---

**Psalm 44**

1 We have heard with our ears, God,
our fathers have told us
what work you did in their days,
in the days of old.
2 You drove out the nations with your hand,
but you planted our people;
you afflicted the peoples,
but you spread our people out in the land.
3 For they did not obtain the land for their possession by their own sword,
neither did their own arm save them;
but your right hand, your arm, and the light of your face,
because you were favorable to them.

4 God, You are my King;
command victory for Jacob.

5 Through you we will push down our adversaries;
through your name we will tread them under,
those who rise up against us.
6 For I will not trust in my bow,
neither will my sword save me.
7 But you have saved us from our adversaries,
and have put to shame those who hate us.
8 In God we have made our boast all the day long,
and we will give thanks to your name forever. Selah

9 But now you have rejected us and brought us dishonor,
and you do not go out with our armies.
10 You make us turn back from the adversary;
and those who hate us take spoil for themselves.
11 You have made us like sheep to be slaughtered
and have scattered us among the nations.
12 You sell your people for nothing;
you have not increased your wealth by doing so.

13 You make us a rebuke to our neighbors,
scoffed and mocked by those around us.
14 You make us an insult among the nations,
a shaking of the head among the peoples.
15 All the day long my dishonor is before me,
and the shame of my face has covered me
16 because of the voice of him who rebukes and insults,
because of the enemy and the avenger.

17 All this has come on us; yet we have not forgotten you
or dealt falsely with your covenant.
18 Our heart has not turned back;
our steps have not gone from your way.
19 Yet you have severely broken us in the place of jackals
and covered us with the shadow of death.

20 If we have forgotten the name of our God
or spread out our hands to a strange god,
21 would not God search this out?
For he knows the secrets of the heart.
22 Indeed, for your sake we are being killed all day long;
we are considered to be sheep for the slaughter.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

23 Awake, why do you sleep, Lord?
Arise, do not reject us forever.
24 Why do you hide your face
and forget our affliction and our oppression?

25 For we have sunk down into the dust;
our bodies cling to the earth.
26 Rise up for our help
and redeem us for the sake of your covenant faithfulness.

---

**Zabura 44**

1 Mun ji da kunnuwanmu, Allah, Kakanninmu suka faɗa mana irin aikin da ka
yi a kwanakinsu, a kwanakin dã. 2 Ka kore al'ummai da hannunka, amma ka
dasa mutanenmu; ka azabci mutane, amma ka baza mutanenmu cikin ƙasar. 3
Gama basu samu mallakar ƙasar ta takobin kansu ba, ba kuma ƙarfin kansu ba
ne ya cece su; amma hannun damanka da ƙarfinka da hasken fuskarka ne,
saboda yi tagomashi gare su. 4 Allah, kai ne sarkina; ka umarta nasara domin
Yakubu. 5 Da taimakonka zamu tura maƙiyanmu; da sunanka za mu tattakesu,
waɗanda suka tashi gãba da mu. 6 Gama ba zan dogara ga bakana ba, takobina
kuma ba zai cece ni ba. 7 Amma ka cece mu daga maƙiyanmu, ka ba masu
ƙinmu kunya. 8 A cikin Allah muke fahariya a kullum, kuma za mu yi godiya ga
sunanka har abada. Selah 9 Amma yanzu ka ƙi mu ka kawo mu ga kunya, kuma
baka yi tafiya tare da mayaƙanmu ba. 10 Ka sa muka juya baya daga maƙiyin;
kuma waɗanda suka ƙi mu suna ɗibi ganima domin kansu. 11 Ka maida mu
kamar tumakin da aka ƙaddara don abinci ka warwatsar da mu cikin al'ummai.
12 Ba a bakin komai ka sayar da mutanenka ba; ba ka ƙara wadatarka ta yin
haka ba. 13 Ka maida mu abin zargi ga maƙwabtanmu, waɗanda ke kewaye da
mu suna yi mana reni da ba'a. 14 Ka sa mun zama abin zãgi cikin al'ummai,
abin girgiza kai cikin tarrukan mutane. 15 A dukkan tsawon rana ƙasƙancina
na gabana, kuma kunyar fuskata ta rufe ni 16 saboda muryar wanda ke
tsautarwa da zage-zage, saboda maƙiyi da mai ɗaukar fansa. 17 Dukkan
waɗannan sun zo a kanmu; duk da haka ba mu mance da kai ba ko kuwa mu yi
aiki cikin rahin gaskiya da alƙawaranka. 18 Zuciyarmu bata juya ba; ƙafafunmu
ba su yi nisa daga hanyarka ba. 19 Duk da haka ka kakkarya mu a wurin diloli
ka rufe mu da inuwar mutuwa. 20 Idan mun mance da sunan Allahnmu ko
kuwa muka buɗe hannuwanmu ga wani bãƙon allah, 21 Allah ba zai bincika
haka ba? Gama ya san asiran zuciya. 22 Hakika, ta dalilinka ake karkashe mu
dukkan rana; ana yi mana kallon tumaki domin yanka. 23 Farka, me yasa kake
barci, Ubangiji? Tashi, kada ka jefar da mu da daɗewa. 24 Me yasa ka ɓoye


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

fuskarka ka mance da matsananciyar azabarmu da wahalarmu? 25 Gama mun
narke mun zama ƙura; jikunanmu sun manne da ƙasa. 26 Tashi tsaye domin
taimakonmu ka 'yantar da mu ta dalilin amintaccen alƙawarinka.

---

**Psalm 45**

1 My heart overflows on a good subject;
I will read aloud the words I have composed about the king;
my tongue is the pen of a ready writer.

2 You are fairer than the children of mankind;
grace is poured onto your lips;
therefore we know that God has blessed you forever.

3 Gird your sword to your side, mighty one,
in your glory and your majesty.
4 In your majesty ride on triumphantly
because of trustworthiness, meekness, and righteousness;
your right hand will teach you fearful things.
5 Your arrows are sharp;
the peoples fall under you;
your arrows are in the hearts of the king's enemies.
6 Your throne, God, is forever and ever;
a scepter of justice is the scepter of your kingdom.
7 You have loved righteousness and hated wickedness;
therefore God, your God, has anointed you
with the oil of gladness more than your companions.
8 All your garments smell of myrrh, aloes, and cassia;
out of ivory palaces
stringed instruments have made you glad.
9 Kings' daughters are among your honorable women;
at your right hand stands the queen clothed in gold of Ophir.

10 Listen, daughter, consider and incline your ear;
forget your own people and your father's house.
11 In this way the king will desire your beauty;
he is your master; revere him.
12 The daughter of Tyre will be there with a gift;
the rich among the people will beg for your favor.
13 The royal daughter in the palace is all glorious;
her clothing is worked with gold.
14 She will be led to the king in embroidered dress;
the virgins, her companions who follow her,

will be brought to you.
15 They will be led by gladness and rejoicing;
they will enter into the king's palace.

16 In the place of your fathers will be your children,
whom you will make princes in all the earth.

17 I will make your name to be remembered in all generations;
therefore the peoples will give you thanks forever and ever.

---

**Zabura 45**

1 Zuciyata na jin daɗi da nagartaccen zance; Zan karanta kalmomin da na
harhaɗo a kan sarki da ƙarfi; harshena shi ne al'ƙalamin shiryayyen marubuci.
2 Ka fi 'ya'yan ɗan Adam kyau; an zuba alheri a leɓunanka; saboda haka mun
san Allah ya albarkaceka har abada. 3 Kasa takobinka a gefenka, mai girma,
cikin ɗaukakarka da martabarka. 4 Cikin darajarka ka hau dokinka cikin murna
saboda yarda da tawali'u da ayyukan adalci; hannun damanka zai koya maka
abubuwan bantsoro. 5 Kibawunka na da ƙaifi; mutane sun faɗa ƙarƙashinka;
kibawunka na cikin zukatan maƙiyan sarki. 6 Kursiyinka, Allah, yana nan har
abada, sandar adalci shi ne sandar mulkinka. 7 Kana ƙaunar ayyukan adalci
kuma kana ƙin mugunta; saboda haka Allah, Allahnka, ya shafe ka da mai na
murna fiye da abokan taraiyarka. 8 Dukkan tufafinka na ƙamshin turaren mur
da aloyes da ƙahonnin da aka samo; daga kowacce fadar hauren giwa kayyakin
busa da kiɗe-kiɗe sun saka murna. 9 'Ya'ya mata na sarakuna na cikin
matayenka masu martaba; sarauniya na tsaye da tufafin zinariya da Ofir a
hannun damanka, 10 Saurara, ɗiya, ki maida hankali ki buɗe kunne, ki mance
da mutanenki da gidan mahaifinki. 11 Ta haka sarkin zai yi marmarin kyanki;
shi shugabanki ne; ki girmama shi. 12 Ɗiyar Taya zata kasance a wurin da
kyauta; masu arziki cikin mutanen za su nemi alfarmarku. 13 Ɗiya gimbiya a
fãda tana cikin dukkan ɗaukaka; an yi aikin tufafinta da zinariya. 14 Za a kaita
wurin sarki cikin kyawawan tufafi masu ado kala-kala; budurwai, ƙawayenta
dake binta, za a kawo maka. 15 Za a jagorance su da murna da farinciki; za su
shiga cikin fadar sarki. 16 A fãdar ubanninka 'ya'yanka zasu kasance, waɗanda
zaka maida su yarimai a dukkan duniya. 17 Zan sa sunanka ya dawwama a
dukkan tsararraki; saboda haka mutanen zasu yi maka godiya har abada
abadin.

---

**Psalm 46**

1 God is our refuge and strength,
a very present help in trouble.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

2 Therefore we will not fear, though the earth should change,
though the mountains should be shaken into the heart of the seas,
3 though its waters roar and rage, and
though the mountains tremble with their swelling. Selah

4 There is a river whose streams make the city of God happy,
the holy place where the Most High dwells.
5 God is in the middle of her; she will not be moved;
God will help her, and he will do so at the dawn of morning.
6 The nations raged and the kingdoms were shaken;
he lifted up his voice, and the earth melted.

7 Yahweh of hosts is with us;
the God of Jacob is our refuge. Selah

8 Come, behold the deeds of Yahweh,
who has set up objects of horror on earth.
9 He makes wars cease to the ends of the earth;
he breaks the bow and cuts the spear into pieces;
he burns up the shields.
10 Be quiet and know that I am God;
I will be exalted among the nations;
I will be exalted on the earth.

11 Yahweh of hosts is with us;
the God of Jacob is our refuge. Selah

---

**Zabura 46**

1 Allah shi ne mafakarmu da ƙarfinmu, Mai matuƙar taimako a lokacin wahala.
2 Domin haka ba za mu ji tsoro ba, ko duniya zata canza, ko an girgiza duwatsu
har cikin tekuna, 3 ko ruwayenta sun yi ruri da tangaɗi, duwatsu kuma suna
motsi saboda kumburinsu. Selah 4 Akwai kogi, da ƙoramu waɗanda ke sa
birnin Allah farinciki, wuri mai tsarki na shirayi na Maɗaukaki. 5 Allah yana
cikin tsakiyarta; ba zata kawu ba; Allah zai taimake ta, kuma zai yi haka da
sassafen safiya. 6 Al'ummai suka fusata kuma mulkoki suka girgiza; ya tayar da
muryarsa, kuma duniya ta narke. 7 Yahweh mai runduna na tare da mu; Allah
na Yakubu shi ne mafakarmu. Selah 8 Zo, dubi ayyukan Yahweh, hallakar da ya
kawo wa duniya. 9 Ya sa yaƙe-yaƙe su ƙare har zuwa iyakar duniya; ya
kakkarya baka ya daddatsa mãsu gutsu--gutsu; ya ƙone garkuwoyi. 10 Ku yi
shiru ku sani Ni ne Allah; Zan sami ɗaukaka a cikin al'ummai; Za a ɗaukaka ni
a duniya. 11 Yahweh mai runduna na tare da mu; Allah na Yakubu ne


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

mafakarmu. Saleh

---

**Psalm 47**

1 Clap your hands, all you peoples;
shout to God with the sound of celebration.

2 For Yahweh Most High is terrifying;
he is a great King over all the earth.
3 He subdues peoples under us
and nations under our feet.
4 He chooses our inheritance for us,
the pride of Jacob whom he loved. Selah

5 God has gone up with a shout,
Yahweh with the sound of a ram's horn.
6 Sing praises to God, sing praises;
sing praises to our King, sing praises.
7 For God is the King over all the earth;
sing praises with understanding.

8 God reigns over the nations;
God sits on his holy throne.
9 The princes of the peoples have gathered together
to the people of the God of Abraham;
for the shields of the earth belong to God;
he is greatly exalted.

---

**Zabura 47**

1 Ku tafa hannuwanku, ku dukkan mutane; ku yi sowa ga Allah da muryar
nasara. 2 Gama Yahweh Maɗaukaki abin tsoro ne; shi Sarki ne mai girma bisa
dukkan duniya. 3 Ya mayar da mutane ƙarƙashinmu, ya sa al'ummai a
ƙarƙƙashin ƙafafunmu. 4 Ya zaɓi gãdonmu dominmu, ɗaukakar Yakubu wanda
ya ke ƙauna. Selah 5 Allah ya tafi sama da sowa, Yahweh da ƙarar kakaki. 6
Raira waƙoƙin yabo ga Allah. raira waƙoƙin yabo; raira waƙoƙin yabo ga
Sarkinmu, raira waƙoƙin yabo. 7 Gama Allah Sarki ne a kan dukkan duniya;
raira woƙoƙin yabo da ganewa. 8 Allah yana mulki a kan al'ummai; Allah na
zaune a tsattsarkan kursiyinsa. 9 'Ya'yan sarakuna sun tattaru wurin mutanen
Allah na Ibrahim; gama garkuwoyin duniya na Allah ne; yana da ɗaukaka mai
girma.

---


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**Psalm 48**

1 Great is Yahweh and greatly to be praised,
in the city of our God on his holy mountain.

2 Beautiful in elevation,
the joy of the whole earth,
is Mount Zion, on the sides of the north,
the city of the great King.
3 God has made himself known in her palaces as a refuge.

4 For, see, the kings assembled themselves;
they passed by together.
5 They saw it, then they were amazed;
they were dismayed, and they hurried away.
6 Trembling took hold of them there,
pain as when a woman is in labor.
7 With the east wind
you break the ships of Tarshish.

8 As we have heard,
so have we seen
in the city of Yahweh of hosts,
in the city of our God;
God will establish it
forever. Selah

9 We have thought about your covenant faithfulness, God,
in the middle of your temple.
10 As your name is, God,
so is your praise to the ends of the earth;
your right hand is full of righteousness.
11 Let Mount Zion be glad,
let the daughters of Judah rejoice
because of your righteous decrees.

12 Walk around Mount Zion, go round about her;
count her towers,
13 notice well her walls,
and look at her palaces
so that you may tell it to the next generation.

14 For this God is our God forever and ever;
he will be our guide to death.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

## Zabura 48

1 Yahweh mai girma ne kuma a yabe shi da girma, cikin birnin Allahnmu a
tsauni mai tsarki. 2 Mai kyakkyawan tsawo, farincikin duk duniya, shi ne
Tsaunin Sihiyona, a kusurwoyin arewa, birnin sarki mai girma. 3 Allah ya maida
kansa sananne a cikin fadodinta a matsayin mafaka. 4 Gama, duba, sarakuna
sun tattaro kansu; suna wucewa tare. 5 Suka gan ta, sa'an nan suka yi mamaki;
suka damu ƙwarai, sai suka wuce da sauri. 6 Firgici ya mamaye su a wurin, da
azaba kamar ta mace mai naƙuda. 7 Da iskar gabas ka karya jiragen ruwan
Tarshish. 8 Kamar yadda muka ji haka muka gani a birnin Yahweh mai
runduna, a birnin Allahnmu; Allah zai kafa shi har abada. Selah 9 Mun yi
tunanin amintaccen alƙawarinka, Allah. a tsakiyar haikalinka. 10 Kamar yadda
sunanka ya ke, Allah, haka yabonka har ga iyakar duniya; hannun damanka na
cike da ayyukan adalci. 11 Tsaunin Sihiyona yi murna, bari 'ya'ya mata na
Yahuda su yi farinciki saboda shari'unka masu adalci. 12 Yi tafiya a kewayen
Dutsen Sihiyona, je ka kewaya ta, harabarta da hasumiyarta, 13 lura da
bangayenta sosai kuma ka duba fãdodinta da kyau, don ka faɗa wa tsara mai
zuwa. 14 Gama wannan Allahn shi ne Allahnmu har abada abadin; shi zai bi
damu har mutuwa.

## Psalm 49

1 Hear this, all you peoples;
give ear, all you inhabitants of the world,
2 both low and high,
rich and poor together.
3 My mouth will speak wisdom
and the meditation of my heart will be of understanding.
4 I will incline my ear to a parable;
I will begin my parable with the harp.

5 Why should I fear the days of evil,
when iniquity surrounds me at my heels?
6 Why should I fear those who trust in their wealth
and boast about the amount of their riches?
7 It is certain that no one can redeem his brother
or give God a ransom for him,
8 For the redemption of one's life is costly,
and no one can pay what we owe.
9 No one can live forever
so that he would not see the pit.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

10 For he will see decay. Wise men die;
the fool and the brute alike perish
and leave their wealth to others.
11 Their inner thought is that their families will continue forever,
and the places where they live, to all generations;
they call their lands after their own names.

12 But man, having wealth, does not remain alive;
he is like the wild animals that perish.

13 This, their way, is their folly;
yet after them, men approve of their sayings. Selah
14 Like sheep they are appointed for Sheol,
and death will be their shepherd.
The upright will rule over them in the morning,
and their bodies will be consumed in Sheol,
with no place for them to live.
15 But God will redeem my life from the power of Sheol;
he will receive me. Selah
16 Do not be afraid when one becomes rich,
and the glory of his house increases.
17 For when he dies he will take nothing away;
his glory will not go down after him.
18 He blessed his soul while he lived—
and men praise you when you live for yourself—
19 he will go to the generation of his fathers
and they will never see the light again.

20 One who has wealth but no understanding
is like the animals that perish.

---

**Zabura 49**

1 Ku ji wannan, dukkanku mutane; ku kasa kunne, dukkanku mazaunan duniya,
ƙanana da manya, 2 masu arziki da matalauta dukka. 3 Bakina zai yi maganar
hikima kuma nazarin zuciyata zai zama na ganewa. 4 Zan sa kunnena ga misali;
zan fara misalina da molo. 5 Me zai sa in ji tsoron kwanakin mugunta, sa'ad da
zunuban maƙiyana suka kewaye ni. 6 Me zai sa in ji tsoron waɗanda suka
dogara ga wadatarsu suke kuma yin fahariya game da arzikinsu? 7 Tabbas
babu wanda zai iya fansar ɗan'uwansa ko ya ba Allah fansa dominsa, 8 Gama
'yantar da ran wani na da tsada, kuma ba wanda zai iya biyan bashinmu. 9
Babu wanda zai dawwama da har jikinsa ba zai ruɓe ba. 10 Gama zai ga ruɓa.

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

Masu hikima na mutuwa; wawaye da sakarkaru ma na lalacewa su kuma bar
wadatarsu ga waɗansu. 11 Tunaninsu na can ciki shi ne iyalansu zasu cigaba
har abada, wuraren da suke zama kuma, su cigaba har dukkan tsararraki; suna
kiran gonakinsu da sunayensu. 12 Amma mutum, mai arziki ba shi rayuwa har
abada; yana kamar dabbobi dake mutuwa. 13 Wannan, hanyarsu, ita ce
wautarsu; duk da haka bayansu, mutane suna amincewa da maganganunsu. 14
Kamar tumaki an ƙaddara su ga Lahira, kuma mutuwa zata zama mai kiwon su.
Adalai zasu yi mulki a kansu da safe, kuma jikunansu zasu hallaka a Lahira,
tare da rashin wurin zama dominsu. 15 Amma Allah zai 'yantar da rai na daga
ikon lahira; zai karɓe ni. Selah 16 Kada ka ji tsoro sa'ad da wani ya yi arziki,
kuma darajar gidansa ta ƙaru. 17 Gama sa'ad da ya mutu ba zai tafi da komai
ba; darajarsa ba zata tafi tare da shi ba sa'ad da ya mutu. 18 Ko da mutum yana
farinciki da nasararsa saboda arzikinsa yayin da ya ke raye- kuma mutane na
yabonka sa'ad da kake rayuwa don kanka- 19 zai tafi zuwa tsarar ubanninsa
kuma ba za su ƙara ganin haske kuma ba. 20 Mai wadata amma ba shi da
ganewa yana kamar dabbobi, dake lalacewa.

---

**Psalm 50**

1 The Mighty One, God, Yahweh,
has spoken and called the earth
from the rising of the sun to its setting.
2 Out of Zion, the perfection of beauty,
God has shone.
3 Our God comes
and does not stay silent;
a fire devours before him,
and it is very stormy around him.
4 He calls to the heavens above
and to the earth so that he may judge his people:
5 "Gather my faithful ones together to me,
those who have made a covenant with me by sacrifice."
6 The heavens will declare his righteousness,
for God himself is judge. Selah

7 "Hear, my people, and I will speak, Israel,
and I will testify against you.
I am God, your God.
8 I will not reprove you for your sacrifices;
your burnt offerings are always before me.
9 I will take no bull out of your house,
or male goats out of your folds.

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

10 For every animal of the forest is mine,
and the cattle on a thousand hills.
11 I know all the birds of the mountains,
and the wild beasts of the field are mine.
12 If I were hungry, I would not tell you;
for the world is mine, and everything in it.
13 Will I eat the flesh of bulls
or drink the blood of goats?

14 Offer to God the sacrifice of thanksgiving,
and pay your vows to the Most High.
15 Call on me in the day of trouble;
I will rescue you, and you will glorify me."

16 But to the wicked God says,
"What have you to do with declaring my statutes,
that you have taken my covenant in your mouth,
17 since you hate instruction
and throw my words away?
18 When you see a thief, you agree with him;
you participate with those who commit adultery.
19 You give your mouth to evil,
and your tongue expresses deceit.
20 You sit and speak against your brother;
you slander your own mother's son.
21 You have done these things, but I have kept silent,
so you thought that I was someone just like yourself.
But I will reprove you
and bring up, right before your eyes, all the things you have done.

22 Give this careful consideration, you who forget God,
otherwise I will tear you to pieces,
and there will be no one to come to help you!
23 The one who offers a sacrifice of thanksgiving praises me,
and to anyone who plans his path in the right way
I will show God's salvation."

---

**Zabura 50**

1 Maɗaukaki, Allah, Yahweh, ya yi magana yana kiran duniya daga fitar rana
zuwa faɗuwarta. 2 Daga Sihiyona, wuri mafi kyau, Allah yana haskakawa. 3
Allahnmu ya zo kuma ba ya tsaye shiru; wuta na ci a gabansa, kuma babban
hadari na kewaye da shi. 4 Ya kira sammai da duniya domin ya shar'anta

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

mutanensa. **5** Tattaro mani amintattuna dukka gare ni, waɗanda suka yi
alƙawari dani ta miƙa hadaya." **6** Sammai zasu yi shelar ayyukan adalcinsa,
gama Allah da kansa alƙali ne. Selah **7** Ku ji, mutanena, kuma zan yi magana;
Ni ne Allah, Allahnku. **8** Ba zan kwaɓe ku domin hadayunku ba; hadayunku na
ƙonawa na gabana kullum. **9** Ba zan ƙarɓi bijimi daga gidanku ba, ko kuwa
bunsurai daga garkenku ba. **10** Gama kowanne naman jeji nawa ne da shanun
kan tuddai dubu. **11** Na san dukkan tsuntsayen duwatsu, kuma namomin jeji na
fili nawa ne. **12** Idan ina jin yunwa, ba zan faɗa maku ba; gama duniya tawa ce,
da dukkan abin da ke cikinta. **13** Ko zan ci naman bijimai ko in sha jinin
awakai? **14** Ku miƙa wa Allah hadayar godiya, kuma ku bada alƙawaranku ta
rantsuwa ga Mai iko dukka. **15** Ku yi kira gare ni a ranar damuwa; Zan cece ku,
kuma zaku girmama ni." **16** Amma ga mugaye Allah yace, "Me zaku yi da
furtawar farillaina, har da zaku ɗauki alƙawarina a bakinku, **17** tunda kun ƙi
umarnina kuma kun jefar da maganganuna? **18** Sa'ad da kuka ga barawo, kuka
yarda da shi; kuna ayyuka tare da waɗanda ke yin zina. **19** Kun bada bakinku
ga mugunta, kuma harshenku na fitar da ruɗu. **20** Ka zauna kana magana gãba
da ɗan'uwanka; ka na saran ɗan mahaifiyarka. **21** Kun aikata waɗannan
abubuwan, amma na yi shiru, sai kuka zata cewa Ni kamarku nake. Amma zan
kwaɓe ku in kawo a gaban idanuwanku, dukkan abubuwan da kuka yi. **22** Ku
lura da wannan da kulawa, ku da kuka mance da Allah, ko kuma zan yayyaga
ku gutsu-gutsu, kuma babu wanda zai zo ya taimake ku! **23** Wanda ya ke miƙa
hadayar godiya yana yabona ne, kuma ga duk wanda ya ke rayuwarsa a hanyar
da ta dace zan nuna masa ceton Allah."

---

**Psalm 51**

**1** Have mercy on me, God,
    because of your covenant faithfulness;
for the sake of the multitude of your merciful actions,
    blot out my transgressions.
**2** Wash me thoroughly from my iniquity
    and cleanse me from my sin.

**3** For I know my transgressions,
    and my sin is always before me.
**4** Against you, you only, I have sinned
    and done what is evil in your sight;
you are justified when you speak;
    you are blameless when you judge.
**5** See, I was born in iniquity;
    as soon as my mother conceived me, I was in sin.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

6 See, you desire trustworthiness in my inner self;
and you teach me wisdom in the secret place within.

7 Purify me with hyssop, and I will be clean;
wash me, and I will be whiter than snow.
8 Make me hear joy and gladness
so that the bones that you have broken may rejoice.
9 Hide your face from my sins
and blot out all my iniquities.

10 Create in me a clean heart, God,
and renew a right spirit within me.
11 Do not drive me away from your presence,
and do not take your holy Spirit from me.
12 Restore to me the joy of your salvation,
and sustain me with a willing spirit.

13 Then will I teach transgressors your ways,
and sinners will be converted to you.
14 Forgive me for shedding blood,
God of my salvation,
and I will shout for the joy of your righteousness.
15 Lord, open my lips,
and my mouth will express your praise.
16 For you do not delight in sacrifice, or I would give it;
you have no pleasure in burnt offerings.
17 The sacrifices of God are a broken spirit.
You, God, will not despise a broken and a contrite heart.

18 Do good in your good pleasure to Zion;
rebuild the walls of Jerusalem.
19 Then will you delight in the sacrifices of righteousness,
in burnt offerings and whole burnt offerings;
then our people will offer bulls on your altar.

---

**Zabura 51**

1 Ka yi mani jinƙai, Allah, saboda amintaccen alƙawarinka; saboda kana yin
ayyukan jinƙai masu yawa, ka tsige kurakuraina. 2 Ka wanke ni sosai daga
zunubina ka share mani laifina. 3 Gama na san kurakuraina, kuma laifina yana
gabana kullum. 4 Gãba da kai, kai kaɗai, na yiwa laifi kuma na yi abin mugunta
a fuskarka; ka yi dai-dai sa'ad da kayi magana; baka yi kuskure ba sa'ad da ka

shar'anta. **5** Duba, An haife ni a cikin zunubi; tun daga cikin mahaifiyata, ina
cikin zunubi. **6** Duba, kana so in yi marmarin aminci cikin zuciyata; a cikin
zuciyata zaka sa in san hikima. **7** Ka tsarkake ni da abin tsarkakewa, zan kuwa
tsarkaka; ka wanke ni, zan kuwa fi auduga fari. **8** Ka sa in ji daɗin rai da murna
saboda ƙasusuwan da ka karya suyi farinciki. **9** Ka ɓoye fuskarka daga laifofina
ka hure dukkan zunubaina. **10** Ka sa in so yi maka biyayya kullum, Allah, ka sa
kullum in so yin abin da ke dai-dai. **11** Kada ka kore ni daga gare ka, kar kuma
ka ɗauke mani Ruhunka Mai Tsarki daga gare ni. **12** Ka maido mani da
farincikin cetonka, ka riƙe ni da ruhun yin biyayya. **13** Sa'an nan zan koya wa
masu zunubi hanyoyinka, masu laifi kuma zasu komo gare ka **14** Ka gafarce ni
domin zub da jini, Allahn cetona, sai in yi sowa domin farincikin ayyukan
adalcinka. **15** Ubangiji, ka buɗe leɓunana, sai bakina ya furta yabonka. **16**
Gama baka murna da sadaka, da zan bada ita; Baka jin daɗin baye-bayen
ƙonawa. **17** Hadayu na Allah sune karyayyen ruhu. Kai, Allah, baza ka ƙi zuciya
mai tuba da kuma tawali'u ba. **18** Kayi nagarta cikin managarcin jin daɗinka ga
Sihiyona; ka sake gina garun Yerusalem. **19** Sa'an nan zaka yi murna da
sadakokin ayyukan aɗalci da baye-bayen ƙonawa da ainihin baye-yen ƙonawa;
sa'an nan mutanenmu zasu miƙa bijimai a bagadinka.

---

**Psalm 52**

**1** Why are you proud of making trouble, you mighty man?
The covenant faithfulness of God comes every day.
**2** Your tongue plans destruction
like a sharp razor, working deceitfully.
**3** You love evil more than good
and lying rather than speaking righteousness. Selah
**4** You love all words that devour others,
you deceitful tongue.

**5** God will surely destroy you forever;
he will take you up and pluck you out of your tent
and root you out of the land of the living. Selah
**6** The righteous will also see it and fear;
they will laugh at him and say,
**7** "See, this is a man who did not make God his refuge,
but he trusted in the abundance of his wealth,
and he was strong when he destroyed others."

**8** But as for me, I am like a green olive tree in the house of God;
I will trust in the covenant faithfulness of God forever and ever.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**9** I will give you thanks forever for what you have done.
I will wait for your name, because it is good,
in the presence of your faithful ones.

---

**Zabura 52**

**1** Meyasa kuke taƙama da tada fitina, ku manyan mutane? Alƙawarin Allah mai
aminci yana zuwa kullum. **2** Harshenku yana shirya hallakarwa kamar reza mai
kaifi, kuna aikata yaudara. **3** Kuna ƙaunar mugunta fiye da nagarta ƙarya kuma
fiye da maganar adalci. Selah **4** Ka na ƙaunar maganar da zata hallaka
waɗansu, kai harshe mai yaudara. **5** Haka Allah zai hallaka ka har abada, zai
ɗauke ka daga rumfarka ya tumɓuke ka daga ƙasar masu rai. Selah. **6** Masu
adalci zasu gani su ji tsoro; su yi masa dariya su ce, **7** "Ku dubi mutumin da bai
mayar da Allah wurin fakewarsa ba, amma ya dogara ga dukiya da yawa, kuma
yana da ƙarfi sa'ad da ya hallaka waɗansu." **8** Amma ni, ina kama da itacen
inabi mai sheƙi a cikin gidan Allah; zan dogara ga alƙawarin Allah mai aminci
har abada. **9** Zan yi godiya gare ka har abada saboda abin da kayi. Zan jira ga
sunanka, saboda yana da kyau a cikin taron jama'arka masu tsoron ka.

---

**Psalm 53**

**1** A fool says in his heart,
"There is no God."
They are corrupt and have done abominable iniquity;
there is no one who does good.

**2** God looks down from heaven
on the children of mankind
to see if there are any who understand,
who seek after him.
**3** They have all turned away. Together they have become corrupt.
There is not one who does good,
not even one.

**4** Do those who behave wickedly have no understanding—
those who devour my people as if they were eating bread
and they do not call on God?
**5** There they are, in great fear,
where there was nothing to cause them to be afraid;
for God will scatter the bones of those who encamp against you;
you put them to shame,
for God has rejected them.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**6** Oh, that the salvation of Israel would come from Zion!
When God brings back his people from the captivity,
then Jacob will rejoice and Israel will be glad!

---

**Zabura 53**

**1** Wawa a zuciyarsa yace, "Babu wani Allah." Dukkan su sun gurɓace sun yi
aikin mugunta; babu ko ɗaya dake aikata abin kirki. **2** Allah ya dubo 'yan Adam
daga sama, ya gani ko akwai wani mai fahimta, wanda ke neman sa. **3** Dukkan
su sun fanɗare. Gabaɗayan su sun gurɓace. Ba wani mai aikata abin kirki, babu
ko guda ɗaya. **4** Waɗanda ke aikata mugunta basu da fahimta ne--waɗanda ke
cin naman mutanena kamar suna cin gurasa kuma ba su kira ga Allah ba? **5**
Suna cikin tsoro mai yawa ko da ya ke ba wani abin tsoratarwa; gama Allah zai
tarwatsa duk wanda ya yi maku kwanto; irin waɗannan mutane zasu sha kunya
gama Allah ya ƙi su. **6** Oh, dama ceton Isra'ila ya zo daga Sihiyona! Sa'ad da
Allah ya dawo da mutanensa daga bauta, Yakubu zai yi farinciki, Isra'ila kuma
zai yi murna!

---

**Psalm 54**

**1** Save me, God, by your name,
and judge me in your might.
**2** Hear my prayer, God;
give ear to the words of my mouth.

**3** For strangers have risen up against me,
and ruthless men have sought after my life;
they have not set God before them. Selah

**4** See, God is my helper;
the Lord is the one who upholds me.
**5** He will repay my enemies with evil;
in your faithfulness, destroy them!

**6** I will sacrifice to you with a freewill offering;
I will give thanks to your name, Yahweh, for it is good.
**7** For he has rescued me from every trouble;
my eye has looked in triumph on my enemies.

---

**Zabura 54**

**1** Ka cece ni ya Allah, ta wurin sunanka, ka yi mani shari'a cikin ƙarfin ikonka.
**2** Allah, ka ji addu'ata, ka saurari kalmomin bakina. **3** Gama bãƙi sun afko mani,

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

lalatattun mutane na neman raina, basu sa Allah a gabansu ba. Selah. 4 Duba,
Allah shi ne mai taimako na, Ubangiji shi ne mai tallafa ta. 5 Zai saka wa
maƙiyana da mugunta; cikin amincinka, ka hallaka su! 6 Zan baka hadaya ta
yardar rai, zan yi godiya ga sunanka, Yahweh gama haka na da kyau. 7 Gama
ya kuɓutar dani daga kowacce damuwa; idona na duban nasara a kan maƙiyana.

---

**Psalm 55**

**1** Give ear to my prayer, God;
and do not hide yourself from my plea.
**2** Pay attention to me and answer me;
I am restless in my troubles
**3** because of the voice of my enemies,
because of the oppression of the wicked;
for they bring trouble on me,
they are hostile to me with wickedness and anger.

**4** My heart trembles within me,
and the terrors of death have fallen on me.
**5** Fear and trembling have come on me,
and horror has overwhelmed me.
**6** I said, "Oh, if only I had wings like a dove!
Then would I fly away and be at rest.
**7** See, then I would wander far away;
I would stay in the wilderness. Selah
**8** I would hurry to a shelter
from the stormy wind and tempest."

**9** Destroy, Lord, and divide their tongue;
for I see violence and strife in the city.
**10** Day and night they go about on its walls;
wickedness and trouble are in the middle of it.
**11** Wickedness is in the middle of it;
oppression and deceit do not leave its streets.

**12** For it was not an enemy who rebuked me,
then I could have borne it;
neither was it he who hated me who raised himself up against me,
then I would have hidden myself from him.
**13** But it was you, a man equal to myself,
my companion and my close friend.
**14** We had sweet fellowship together;


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

we walked in the house of God with the throng.

**15** Let death come deceitfully on them;
let them go down alive to Sheol,
for wickedness is where they live, right among them.

**16** As for me, I will call on God,
and Yahweh will save me.
**17** In the evening, morning, and at noonday I complain and moan;
he will hear my voice.
**18** He will safely rescue my life from the battle that was against me,
for those who fought against me were many.
**19** God, the one who rules from eternity,
will hear them and humiliate them. Selah

They never change,
and they do not fear God.
**20** My friend has raised his hands against those who were at peace with him;

he has not respected the covenant that he had.
**21** His mouth was smooth as butter,
but his heart was hostile;
his words were softer than oil,
yet they were actually drawn swords.

**22** Place your burdens on Yahweh,
and he will sustain you;
he will never allow a righteous person to totter.
**23** But you, God, will bring the wicked down into the pit of destruction;
men of bloodshed and deceit will not live even half as long as others,
but I will trust in you.

---

## Zabura 55

**1** Allah, ka ji addu'ata, kada ka ɓoye kanka daga roƙona. **2** Ka saurare ni ka
amsa mani, gama bani da hutu cikin wahaluna, **3** saboda muryar maƙiyana,
saboda matsin masu mugunta, gama suna tsananta mani cikin fushi. **4** Zuciyata
tana kiɗima a cikina, tsoron mutuwa ya faɗo kaina. **5** Firgita da razana sun zo
kaina, kuma fargaba ya sha kaina. **6** Na ce, "Oh, dãma ina da fukafukai kamar
kurciya! Da na tashi in je in huta. **7** Da zan tafi can nesa in zauna a cikin jeji.
Selah **8** Da zan yi hanzari in sami mafaka daga hadari mai iska da guguwa. **9**
Ka haɗiye su, Ubangiji, kasa ruɗami cikin harsunansu! Gama na ga ta'addanci
da hargitsi a cikin birnin. **10** Suna ta yawo a kan ganuwarsa dare da rana.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

Mugunta da lalata suna cikin tsakiyarsa. 11 Aikin mugunta na cikin tsakiyarsu;
Tsanani da zamba ba su bar hanyoyinsu ba. 12 Gama da maƙiyi ne ke tsauta
mani, da na iya jurewa; ba kuma wanda ya ke gaba dani ne ya tada kansa gaba
dani ba, da na ɓoye kaina daga wurin sa. 13 Amma kai ne mutum kamar ni,
abokina, da aminina kuma. 14 Mun yi zumunci mai kyau tare, mun je gidan
Yahweh tare da ƙarfafa. 15 Bari mutuwa ta afko masu, bara su gangara lahira,
gama mugunta ce kaɗai rayuwarsu, haka suke. 16 Ni kuwa zan kira ga Allah,
Yahweh zai cece ni. 17 Ko da yamma ko da rana ko da safe, idan na yi ƙara da
nishi zai ji muryata. 18 Zai kuɓutar da raina daga masu kawo mani hari, gama
waɗanda ke faɗa dani suna da yawa. 19 Yahweh, wanda ya ke mulki tun daga
farko, zai ji su ya ƙasƙantar dasu. Ba zasu taɓa canzawa ba, kuma ba sa tsoron
Yahweh. 20 Abokina ya tada hannuwansa gaba da waɗanda ke zaman salama
dani. Bai cika alƙawarin da ya yi ba. 21 Bakinsa yana da taushi kamar mai,
amma zuciyarsa tana da hasala; kalmominsa suna da taushi kamar mai, amma
a gaskiya takubba ne zararru. 22 Ka ɗora wa Yahweh matsalolinka, shi zai riƙe
ka, ba zai bari adalai su lalace ba. 23 Amma kai Allah, za ka kawo miyagu cikin
ramin hallakarwa. Masu shan jini da mayaudaran mutane ba za su rayu koda
kamar na rabin sauran mutane ba, amma zan dogara gare ka.

---

**Psalm 56**

1 Be merciful to me, God,
for men are attacking me!
All the day long those who fight me oppress me.
2 My enemies trample me all day long;
for there are many who arrogantly fight against me.

3 When I am afraid,
I will put my trust in you.
4 In God, whose word I praise—
in God I have put my trust; I will not be afraid;
what can mere man do to me?

5 All the day long they twist my words;
all their thoughts are against me for evil.
6 They gather themselves together, they hide themselves,
and they mark my steps,
just as they have waited for my life.
7 Do not let them escape doing iniquity.
Bring down the peoples in your anger, God.

8 You number my wanderings


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

and put my tears into your bottle;
are they not in your book?
9 Then my enemies will turn back on the day that I call to you;
this I know, that God is for me.

10 In God—whose word I praise,
in Yahweh—whose word I praise,
11 in God I trust,
I will not be afraid.
What can anyone do to me?

12 The duty to fulfill my vows to you is on me, God;
I will give thank offerings to you.
13 For you have rescued my life from death;
you have kept my feet from stumbling,
so that I may walk before God
in the light of the living.

---

**Zabura 56**

1 Ka ji ƙaina ya Allah, gama mutane na kawo mani hari! Dukkan yini suna
tsananta ɓatancin da suke yi mani. 2 Maƙiyana na musguna mani dukkan yini,
gama waɗanda ke yin faɗa dani cikin wauta suna da yawa. 3 Sa'anda na ji
tsoro, zan dogara gare ka. 4 Ina jin daɗin maganar Allah, ga Allah zan dogara;
ba zan ji tsoro ba; me mutum kawai zai iya yi ma ni? 5 Juya maganata suke yi
dukkan yini, dukkan tunaninsu a kaina na mugunta ne. 6 Sun tattara kansu,
sun yi kwanto, suna bin sawuna, suna neman raina. 7 Kada ka bari su dena yin
mugunta. Ya Allah, ka kayar da su a cikin fushinka. 8 Ka lissafa yawace-
yawacena ka kuma sa hawayena cikin kwalba; ko ba a cikin littafinka suke ba?
9 Sa'ad da na kira ka, maƙiyana zasu koma da baya, abin da na sani kenan,
Allah yana tare da ni. 10 A cikin Allah --wanda maganarsa nake yabo, a cikin
Yahweh-- 11 a cikin Allah na dogara, bazan ji tsoro ba. Me wani zai iya yi mani?
12 Aikina shi ne in cika wa'adina gare ka, Yahweh. Zan miƙa baye-baye na
godiya a gare ka. 13 Gama ka kuɓutar da raina daga mutuwa, ka tsare ƙafafuna
daga faɗuwa, domin in yi tafiya a gaban Allah a cikin masu rai.

---

**Psalm 57**

1 Be merciful to me, God, be merciful to me,
for I take refuge in you until these troubles are over.
I stay under your wings for protection
until this destruction is over.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

2 I will cry to God Most High,
to God, who does all things for me.
3 He will send help from heaven and save me,
he rebukes those who hotly pursue me. Selah
God will send me his steadfast love and his faithfulness.

4 My life is among lions;
I am among those who are ready to devour me.
I am among people whose teeth are spears and arrows,
and whose tongues are sharp swords.

5 Be exalted, God, above the heavens;
let your glory be above all the earth.

6 They spread out a net for my feet;
I was bowed down.
They dug a pit in front of me.
They themselves have fallen into the middle of it! Selah

7 My heart is fixed, God, my heart is fixed;
I will sing, yes, I will sing praises.
8 Wake up, my glory!
Wake up, lute and harp!
I will wake up the dawn!

9 I will give thanks to you, Lord, among the peoples;
I will sing praises to you among the nations.
10 For great is your unfailing love, reaching to the heavens;
and your faithfulness to the clouds.

11 Be exalted, God, above the heavens;
may your glory be exalted over all the earth.

---

**Zabura 57**

1 Ka yi mani jinƙai, Yahweh, ka yi mani jinƙai, gama na fake wurin ka har sai
waɗannan wahalu sun wuce. Na tsaya a ƙarƙashin inuwar fukafukanka har sai
wannan hallaka ta ƙare. 2 Zan yi kuka ga Allah Maɗaukaki, ga Allah, wanda ya
ke yi mani komai. 3 Zai aiko da taimako daga sama ya cece ni, yana jin haushin
waɗanda ke ƙuje ni. Allah zai aiko mani da jinƙansa da amincinsa. 4 Raina yana
cikin zakuna, ina cikin waɗanda suke a shirye su cinye ni. Ina cikin mutanen da
haƙoransu māsu ne da kibau, haƙoransu kuma kamar takubba masu kaifi. 5 Ya


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

Yahweh, ka ɗaukaka a bisa sammai, bari ɗaukakarka ta zama a bisa duniya. 6
Sun baza taru saboda ƙafafuna; Na shiga cikin ƙunci. Sun gina rami a gabana.
Amma su da kansu ne suka faɗa a cikin tsakiyarsa! Selah 7 Zuciyata ta kafu,
Allah, zuciyata a kafe take; Zan raira, I, zan raira yabbai. 8 Tashi, ke zuciyata
mai daraja, tashi, ke sarewa da molo, nima tun da asuba zan tashi. 9 A cikin
jama'a zan yi maka godiya, ya Ubangiji; zan raira yabo gare ka a cikin
al'ummai. 10 Gama ƙaunarka tana da girma ƙwarai, ta kai har sama, amincika
kuma ya kai gizagizai. 11 Ka ɗaukaka ya Allah, sama da sammai, darajarka ta
ɗaukaka bisa dukkan duniya.

---

**Psalm 58**

1 Do you rulers speak righteousness?
Do you judge uprightly, you people?
2 No, you commit wickedness in your heart;
you distribute violence throughout the land with your hands.

3 The wicked go astray even when they are in the womb;
they go astray from birth, speaking lies.
4 Their poison is like a snake's poison;
they are like a deaf asp that stops up its ears,
5 that pays no attention to the voice of charmers,
no matter how skillful they are.

6 Shatter their teeth in their mouths, God;
break out the great teeth of the young lions, Yahweh.
7 Let them melt away as water that runs off;
when they shoot their arrows, let them be as though they had no points.
8 Let them be like a snail that melts and passes away,
like the untimely born child of a woman that never sees the sunlight.

9 Before your pots can feel the thorn's burning heat,
he will take them away with a whirlwind,
the green thorns and the burning thorns alike.
10 The righteous will rejoice when he sees God's vengeance;
he will wash his feet in the blood of the wicked,
11 so that men will say,
"Truly, there is a reward for the righteous person;
truly there is a God who judges the earth."

---

**Zabura 58**

1 Ku shugabanni kuna faɗin gaskiya? Ku jama'a kuna yin shari'ar gaskiya? 2

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

Babu, kun yi aikin mugunta cikin zuciyarku; kun baza tashin hankali da
hannuwanku a cikin ƙasar dukka. **3** Tun daga cikin ciki, masu mugunta ke
fanɗarewa, tun daga haihuwarsu suke ratsewa, suna faɗin ƙarya. **4** Dafinsu
kamar dafin maciji ya ke, suna kama da kurmar ƙasa wadda take toshe
kunnuwanta, **5** wadda bata jin muryar masu layu, komai gwanintarsu. **6** Ka
karairaya haƙoransu a cikin bakunansu, ya Allah; ka ciccire manyan haƙoran
'yan zakuna, ya Yahweh. **7** Bari su narke kamar ruwan dake gangarewa; idan
suka harba kibansu, bari su zama kamar basu yi saiti ba. **8** Bari su zama kamar
dodon koɗi wanda ke narkewa ya lalace, kamar jaririn da mace ta haifa kafin
lokacinsa yayi wanda bai taɓa ganin hasken rana ba. **9** Kafin tukunyarka ta ji
zafin wuta, zai kwashe su da guguwa, da ɗanye da wanda a ke ƙonawa dukka.
**10** Mai adalci zai yi farinciki sa'ad da ya ga ramako daga Allah, zai wanke
ƙafafunsa da jinin masu mugunta, **11** domin mutane su ce, "Gaskiya ne akwai
lada ga mutum mai adalci, gaskiya ne akwai Allah wanda ke shar'anta duniya.

---

**Psalm 59**

**1** Rescue me from my enemies, my God;
set me on high away from those who rise up against me.
**2** Keep me safe from those who behave wickedly,
and save me from men of bloodshed.

**3** For, see, they wait in ambush to take my life.
The powerful men gather themselves together against me,
but not because of my transgression or my sin, Yahweh.
**4** For no guilt of mine they prepare to run at me;
awake and help me and see.
**5** You, Yahweh God of hosts,
the God of Israel,
arise and punish all the nations;
do not be merciful to any wicked transgressors. Selah

**6** They return at evening, they howl like dogs
and go around the city.
**7** See, they belch out with their mouths;
swords are in their lips,
for they say, "Who hears us?"
**8** But you, Yahweh, laugh at them;
you mock at all the nations.

**9** God, my strength, I will pay attention to you;
you are my high tower.
**10** My God will meet me with his covenant faithfulness;


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

God will let me see my desire on my enemies.

**11** Do not kill them,
or my people will forget.
Scatter them by your power and make them fall,
Lord our shield.
**12** For the sins of their mouths and the words of their lips,
let them be captured in their pride,
and for the curses and lies that they express.
**13** Consume them in wrath,
consume them so that they will be no more;
let them know that God rules in Jacob
and to the ends of the earth. Selah

**14** At evening they return,
howling like dogs going around the city.
**15** They wander about looking for food
and they growl like a dog if they are not satisfied.
**16** But I will sing about your strength,
and in the morning I will praise your steadfast love!
For you have been my high tower
and a refuge in the day of my distress.

**17** To you, my strength, I will sing praises;
for God is my high tower, the God of covenant faithfulness.

---

**Zabura 59**

**1** Ka kuɓutar dani daga maƙiyana, ya Allahna; ka ɗora ni can sama nesa daga
waɗanda suke taso mani. **2** Ka tsare ni daga waɗanda suke aikata mugunta, ka
cece ni daga mutane waɗanda suke zubar da jini. **3** Gama, duba, sun yi kwanto
domin su ɗauki raina. Manya manyan masu aika mugunta sun tattara kansu
gãba dani, amma ba saboda nayi kuskure ko zunubi ba, Yahweh. **4** Sun shirya
domin su tattake ni ba tare da laifina ba, duba, tashi ka taimake ni. **5** Kai
Yahweh, Allah Mai Runduna, Allah na Isra'ila, tashi ka hori dukkan al'ummai.
Kada ka ji tausan wani mai laifin aika mugunta ko ɗaya. **6** Sukan dawo da
yamma, su zagaya birnin suna haushi kamar karnuka. **7** Duba suna yin gyatsa
da bakunansu, takubba suna kan leɓunansu, suna cewa, "Wane ne ya ke
sauraren mu?" **8** Amma kai, Yahweh, kana yi masu dariya, dukkan al'ummai ba
a bakin komai suke a gare ka ba. **9** Allah, ƙarfina, zan kasa kunne gare ka,
kaine hasumiyata mai tsawo. **10** Allahna zai same ni da alƙawarin amincinsa,
Yahweh, zai biya muradina a kan maƙiyana. **11** Kada ka kashe su domin kada

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

jama'ata su mance. Yahweh, garkuwarmu, ka warwatsa su, ka sa su faɗi. 12
Saboda kalmomin bakinsa, da maganar leɓunansu, ka bari a kwashe su cikin
girman kansu, kuma saboda la'ana da ƙarairayin da suka bayyana. 13 Ka
hallaka su cikin hasalarka, ka hallaka su domin kada su ƙara kasancewa. Bari
su sani, Allah ne ke mulki cikin Yakubu kuma har iyakar duniya. Selah 14
Sukan dawo da yamma, su zagaya birnin suna haushi kamar karnuka. 15 Sukan
yi yawo suna neman abinci, sukan yi gurnani idan ba su ƙoshi ba. 16 Amma zan
yi rairawa game da ƙarfinka, da safe kuma zan yi rairawa saboda ƙaunarka
madawwamiya! Gama ka zama hasumiyata mai tsawo, mafaka a lokacin dani ke
cikin matsala. 17 A gare ka ƙarfina zan raira yabo, gama Yahweh ne
hasumiyata mai tsawo, Allah mai amincin alƙawari.

---

**Psalm 60**

**1** God, you have rejected us; you have broken through our defenses;
you have been angry; restore us again.

**2** You have made the land tremble; you have torn it apart;
heal its cracks, for it is shaking.

**3** You have made your people see difficult things;
you have made us drink the wine of staggering.

**4** For those who honor you,
you have set up a banner
to be displayed against those who carry the bow. Selah

**5** So that those you love may be rescued,
rescue us with your right hand and answer me.

**6** God has spoken in his holiness, "I will rejoice;
I will divide Shechem
and apportion out the Valley of Sukkoth.

**7** Gilead is mine, and Manasseh is mine;
Ephraim also is my helmet;
Judah is my scepter.

**8** Moab is my washbasin;
over Edom I will throw my sandal;
I will shout in triumph because of Philistia."

**9** Who will bring me into the strong city?
Who will lead me to Edom?

**10** But you, God, have you not rejected us?
You do not go into battle with our army.

**11** Give us help against the enemy,
for man's help is futile.

**12** We will triumph with God's help;


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

he will trample down our enemies.

---

**Zabura 60**

1 Yahweh, ka yashe mu, ka kutsa cikin matsararmu, ka yi fushi, ka dawo da mu.
2 Kasa ƙasar ta girgiza, ka ɓarke ta; tana girgiza, ka warkar da ɓarakarta. 3
Kasa mutanenka su ga abubuwa masu wuya, kasa mun sha ruwan inabin
tangaɗi. 4 Saboda waɗanda ke darjantaka, kasa an tada tuta gãba da masu
ɗaukar baka. 5 Saboda waɗanda kake ƙauna su kuɓuta, ka amsa mani ka
kuɓutar da mu da hannun damanka. 6 Allah ya yi magana cikin tsarkinsa, "Zan
yi farinciki, zan raba Shekem, zan karkasa Kwarin Sukot. 7 Giliyad tawa ce
Manasse ma tawa ce, Ifraim kuma hular kwanona ce, Yahuda kuma sandar
girmana ce. 8 Mowab bangajin wankina ne, zan ajiye takalmina a kan Idom,
zan yi sowa ta murna saboda Filistiya." 9 Wa zai kawo ni birni mai ƙarfi? Wa zai
kai ni Idom? 10 Amma kai Yahweh, ba ka yashe mu ba? Gama ba ka tafi yaƙi
tare da sojojinmu ba. 11 Ka taimake mu gãba da maƙiyanmu gama taimakon
mutum banza ne. 12 Da taimakon Allah za mu yi nasara; shi zai tattake
maƙiyanmu.

---

**Psalm 61**

1 Hear my cry, God;
attend to my prayer.

2 From the ends of the earth will I call to you when my heart is faint;
lead me to the rock that is higher than I.
3 For you have been a refuge for me,
a strong tower from the enemy.

4 Let me live in your tabernacle forever!
Let me take refuge under the shelter of your wings. Selah
5 For you, God, have heard my vows,
you have given me the inheritance of those who honor your name.

6 You will prolong the king's life;
his years will be like many generations.
7 He will reign before God forever;
appoint your steadfast love and faithfulness to protect him.
8 I will sing praise to your name forever
so that I may perform my vows every day. 2

---

**Zabura 61**

1 Ka ji kukana Yahweh, ka amsa addu'ata. 2 Daga iyakar duniya zan kira gare
ka lokacin da zuciyata ta ruɗe, ka kai ni wurin dutsen da ya fi ni tsawo. 3 Gama
kai ne mafakata, hasumiya mai ƙarfi daga maƙiyana. 4 Ka bar ni in zauna a
shirayinka har abada! Ka bar ni in ɓoye cikin inuwar fukafukanka. Selah 5
Gama kai Allah, ka ji wa'adina, ka bani gãdon waɗanda suke darjanta sunanka.
6 Za ka sa ran sarki ya yi tsawo, shekarunsa kuma kamar tsararraki da yawa. 7
Zai kasance a gaban Yahweh har abada. 8 Zan raira yabo ga sunanka har
abada, domin in cika wa'dina gare ka kowacce rana.

---

**Psalm 62**

1 I wait in silence for God alone;
my salvation comes from him.
2 He alone is my rock and my salvation;
he is my high tower;
I will not be greatly moved.

3 How long, all of you, will you attack a man,
that you may murder him,
like a leaning wall or a shaky fence?
4 They consult with him
only to bring him down from his honorable position;
they love to tell lies;
they bless him with their mouths,
but in their hearts they curse him. Selah

5 I wait in silence for God alone;
for my hope is set on him.
6 He alone is my rock and my salvation;
he is my high tower; I will not be moved.
7 With God is my salvation and my glory;
the rock of my strength and my refuge are in God.
8 Trust in him at all times, you people;
pour out your heart before him;
God is a refuge for us. Selah

9 Surely men of low standing are vanity,
and men of high standing are a lie;
they will weigh lightly in the scales;
weighed together, they are lighter than nothing.
10 Do not trust in oppression or robbery;
and do not hope uselessly in riches,
for they will bear no fruit;

do not fix your heart on them.

11 God has spoken once,
twice have I heard this:
power belongs to God.
12 Also to you, Lord, belongs covenant faithfulness,
for you pay back every person for what he has done.

---

**Zabura 62**

1 Na yi shiru a gaban Yahweh kaɗai, daga wurin sa cetona ya ke zuwa. 2 Shi
kaɗai ne cetona, shi ne hasumiyata mai tsawo, ba zan girgiza ba sosai. 3 Har
yaushe ku dukka, zaku kai hari ga mutum ɗaya? Domin ku rufe shi kamar
bangon da a ke jigina da shi, shinge mai rawa? 4 Suna shawara da shi ne domin
su ture shi daga matsayinsa mai daraja kaɗai; su na ƙaunar faɗin ƙarya, suna
sa masa albarka da bakinsu, amma cikin zuciyarsu suna la'antar sa. Selah 5 Ga
Allah kaɗai nake saurare, gama shi ne begena. 6 Shi kaɗai ne dutsena da
cetona, shi ne hasumiyata mai tsawo ba zan jijjigu ba. 7 Allah ne cetona da
ɗaukakata, dutsen ƙarfina da mafakata a cikin Allah suke. 8 Ku dogara gare shi
kowanne lokaci, ku mutane, ku kafa zuciyarku a gaban sa, Allah shi ne
mafakarmu. Selah 9 Ba shakka mutanen da basu da matsayi ba komai bane,
waɗanda ke da matsayin kuma ƙarya ne. Idan a ka auna su a ma'auni ba su da
nauyi, inda za a haɗa su a auna ba su da nauyin komai. 10 Kada ku dogara ga
aikin zalunci ko ƙwace, kada ku sa begenku ga dukiyar wofi, gama ba su da
amfanin komai, kada ku sa zuciya gare su. 11 Allah ya yi magana sau ɗaya, sau
biyu kuwa na ji wannan: iko na Allah ne. 12 Kuma Ubangiji, a gare ka
alƙawarin gaskiya yake. Gama kana ramawa kowanne mutum bisa ga abin da
ya yi.

---

**Psalm 63**

1 God, you are my God!
I earnestly search for you,
my soul thirsts for you,
and my flesh longs for you,
in a dry and weary land
where there is no water.

2 So I have looked on you in the sanctuary,
to see your power and your glory.
3 Because your covenant faithfulness is better than life,
my lips will praise you.
4 So I will bless you while I live;

I will lift up my hands in your name.
5 It will be as if I ate a meal of marrow and fatness;
with joyful lips my mouth will praise you,

6 when I think about you on my bed
and meditate on you in the night watches.
7 For you have been my help,
and in the shadow of your wings I rejoice.
8 I cling to you;
your right hand supports me.

9 But those who seek to destroy my life
will go down into the lowest parts of the earth;
10 they will be given over to those whose hands use the sword,
and they will become food for the jackals.
11 But the king will rejoice in God;
everyone who swears by him will be proud of him,
but the mouth of those who speak lies will be stopped up.

---

**Zabura 63**

1 Allah, kai ne Allahna, da gaske raina ya ke neman ka, raina yana ƙishin ka,
jikina ya ƙagara ya gan ka, a cikin ƙasa da turɓaya in da babu ruwa. 2 Na dubo
zuwa gare ka a cikin mutane masu tsarki domin in ga ikonka da ɗaukakarka. 3
Saboda alƙawarin ka mai aminci yafi rai, leɓunana zasu yabe ka. 4 Zan
albarkace ka sa'ad da nake da rai, a cikin sunanka zan tada hannuwana. 5 Zai
zama kamar na ci abinci mai ɓargo da kitse, zan yabe ka da leɓuna masu
farinciki, 6 sa'ad da ni ke tunaninka a kan gadona, sa'ad da nake nazarin ka a
cikin dare. 7 Gama kai ne taimakona, a ƙarƙashin inuwar fukafukanka nake yin
farinciki. 8 Na manne maka hannun damanka yana tallafa ta. 9 Amma waɗanda
ke nema su hallaka raina, zasu faɗa cikin wuri mai zurfi na duniya; 10 za a
bashe su ga hannun masu aiki da takobi, zasu zama abicin diloli. 11 Amma
sarki zai yi farinciki cikin Allah, dukkan wanda ya rantse da shi, zai yi fahariya
da shi kuma, amma bakin masu faɗin ƙarya za a kwaɓe shi.

---

**Psalm 64**

1 Hear my voice, God, listen to my complaint;
preserve my life from fear of my enemies.

2 Hide me from the secret plotting of evildoers,
from the commotion of those who behave wickedly.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

3 They have sharpened their tongues like swords;
they have aimed their arrows, bitter words,
4 so that they may shoot from secret places at someone who is innocent;
suddenly they shoot at him and fear nothing.

5 They encourage themselves in an evil plan;
they consult privately together in order to set traps;
they say, "Who will see us?"
6 They invent injustices;
"We have finished," they say, "a careful plan."
The inner thoughts and hearts of man are deep.

7 But God will shoot them;
suddenly they will be wounded with his arrows.
8 They will be made to stumble, since their own tongues are against them;
all who see them will wag their heads.
9 All people will fear
and will declare God's deeds.
They will wisely think about what he has done.

10 The righteous will be glad about Yahweh and will take refuge in him;
all the upright in heart will take pride in him.

---

**Zabura 64**

1 Ka ji muryata, Allah, ka saurari ƙarata; ka tsare raina daga tsoron maƙiyana.
2 Ka ɓoye ni daga shirin miyagu, daga hargowar masu aika mugunta. 3 Sun
wasa harsunansu kamar takubba, sun haro kibansu, wato maganganu masu
ɗaci, 4 domin su harbi wanda ba shi da laifi daga wurin da suke ɓoye, nan da
nan suka harbe shi ba tare da sun ji tsoro ba. 5 Suna ƙarfafa kansu cikin shirya
mugunta, suna shawara a asirce domin su ɗana tarkuna, suna cewa, "Wa zai
gan mu?" 6 Suna ƙulla mugunta; "Mun gama" suka ce, "Natsastsen shiri"
Tunanin ciki da zuciyar mutum suna da zurfi. 7 Amma Yahweh, zai harbe su,
nan da nan kibau zasu ji masu ciwo. 8 Zasu yi tuntuɓe tun da ya ke harshensu
yana gãba da su; dukkan waɗanda suka gan su zasu kaɗa kansu. 9 Dukkan
mutane zasu ji tsoro su bayyana ayyukan Allah. Cikin hikima zasu yi tunani a
kan abin da ya yi. 10 Masu adalci zasu yi murna da Yahweh, zasu sami mafaka
a wurinsa. Dukkan waɗanda ke tafiya dai-dai zasu yi fahariya a cikin sa.

---

**Psalm 65**

1 For you, God in Zion, our praise waits;
our vows will be carried out to you.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

2 You who hear prayer,
to you all flesh will come.
3 Iniquities prevail against us;
as for our transgressions, you will forgive them.
4 Blessed is the man whom you choose to bring near to you
so that he may live in your courts.
We will be satisfied with the goodness of your house,
your holy temple.

5 In righteousness you will answer us by doing awesome deeds,
God of our salvation;
you who are hope of all the ends of the earth
and of those who are far across the sea.
6 For it is you who made the mountains firm,
you who are girded with strength.
7 It is you who quiet the roaring of the seas,
the roaring of their waves,
and the commotion of the peoples.
8 Those who live in the uttermost parts of the earth
are afraid of the evidence of your deeds;
you make the east and the west rejoice.

9 You come to help the earth; you water it;
you greatly enrich it;
the river of God is full of water;
you provide mankind grain when you have prepared the earth.
10 You water its furrows abundantly;
you settle down the furrows' ridges;
you make them soft with rain showers;
you bless the sprouts between them.
11 You crown the year with your goodness,
and your wagon tracks overflow with abundance.
12 The pastures in the wilderness drip with dew,
and the hills are girded with joy.
13 The pastures are clothed with flocks;
the valleys also are covered over with grain;
they shout for joy, and they sing.

---

**Zabura 65**

1 Domin kai Allah a Sihiyona ne, yabonmu; da wa'adodinmu, za a kawo maka su
a cikin Sihiyona. 2 Kai da kake jin addu'a, a gare ka dukkan mutane za su zo. 3
Laifofi sun yi mana tsayayya, amma za ka gafarta zunubanmu, za ka kuma
gafarta su. 4 Mai albarka ne mutumin daka zaɓa ya zo ya zauna a kusa da kai a

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

cikin harabarka. Za mu gamsu da kyawawan abubuwan dake a gidanka,
haikalinka mai tsarki. 5 Cikin adalci za ka amsa mana ka yi abubuwan mamaki,
kai Allah na cetonmu, Kai wanda dukkan mutane ke dagara gake ka har da
waɗanda ke a can hayin teku. 6 Gama kai ne ka kafa duwatsu suka yi ƙarfi, kai
wanda ka yi ɗamara da iko. 7 Kai ne ka kwantar da rurin tekuna da
balalloƙansu da hargowar mutane 8 Su waɗanda ke zama a can ƙarshen duniya
suna jin tsoron alamun ayyukanka, kasa gabas da yamma suna farinciki. 9 Ka
zo domin ka taimaki duniya; ka yi mata banruwa, kasa ta yi arziki, kogin Allah
na cike da ruwa; tun da ka hallicci duniya ka tanadawa ɗan Adam hatsi. 10 Ka
jiƙe kwarin kunyai a wadace, ka dai-daita kwarin kunyai sosai, kakan sa su yi
taushi, kasa albarka a kan yabanyarsu. 11 Ka yi wa shekara dajiyar alherai,
sawayen karusanka suka zubo da kitse a kan duniya. 12 Wuraren kiwo a jeji
sun jiƙe da raɓa, ka sa tsire--tsire suyi farinciki. 13 Wuraren kiwo sun cika da
garkuna, kwarurruka sun cika da hatsi, suna shewa ta farinciki, suna rairawa.

---

**Psalm 66**

1 Shout out loud to God, all the earth;
2 Sing out the glory of his name;
make his praise glorious.
3 Say to God, "How terrifying are your deeds!
By the greatness of your power
your enemies will submit to you.
4 All the earth will worship you
and will sing to you;
they will sing praises to your name." Selah

5 Come and see the works of God;
he is fearsome in his deeds toward the sons of mankind.
6 He turned the sea into dry land;
they went through the river on foot;
there we rejoiced in him.
7 He rules forever by his might;
his eyes observe the nations;
let not the rebellious exalt themselves. Selah

8 Give blessing to God, you people,
let the sound of his praise be heard.
9 He keeps us among the living,
and he does not permit our feet to slip.
10 For you, God, have tested us;
you have tested us as silver is tested.


generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**11** You brought us into a net;
you laid a heavy burden on our backs.
**12** You made people ride over our heads;
we went through fire and water,
but you brought us out into a spacious place.

**13** I will come into your house with burnt offerings;
I will pay you my vows
**14** which my lips promised
and my mouth spoke when I was in distress.
**15** I will offer to you burnt offerings of fat animals
with the sweet aroma of rams;
I will offer bulls and goats. Selah

**16** Come and listen, all you who fear God,
and I will declare what he has done for my soul.
**17** I cried to him with my mouth,
and he was praised with my tongue.
**18** If I had seen wickedness within my heart,
the Lord would not have listened to me.
**19** But God has truly heard;
he has paid attention to the voice of my prayer.
**20** Blessed be God,
who has not turned away my prayer
or his covenant faithfulness from me.

---

**Zabura 66**

**1** Ku yi sowa ta farinciki ga Yahweh, ku duniya dukka. **2** Ku raira ɗaukakar
sunansa, ku sa yabonsa ya zama ɗaukakakke. **3** Ku ce da Allah, "Ayyukanka
suna da ban tsoro! Da girman ikonka kasa maƙiyanka su yi ladabi a gabanka. **4**
Dukkan duniya zasu bauta maka su raira yabo gare ka, zasu yi rairawa ga
sunanka." Selah **5** Ku zo ku ga ayyukan Yahweh, ayyukansa na da ban mamaki
ga 'yan Adam. **6** Ya mayar da teku busasshiyar ƙasa; sun bi ta cikin teku da
ƙafa; can muka yi farinciki a cikin sa. **7** Da ikonsa ya ke mulki har abada,
idanunsa suna lura da al'ummai; kada masu tawaye su ɗaukaka kansu. Selah **8**
Ku albarkaci Allah, ku mutane, bari a ji amon yabonsa. **9** Ya bar mu cikin masu
rai, bai bari ƙafafunmu suka yi tuntuɓe ba. **10** Gama kai Yahweh ka gwada mu,
ka gwada mu kamar yadda a ke gwada azurfa. **11** Ka kawo mu cikin taru, ka
ɗora mana kaya mai nauyi a kanmu. **12** Ka bari mutane su tattaka mu, mun
shiga cikin wuta da ruwa, amma ka kawo mu cikin wuri mai faɗi. **13** Zan zo

 

cikin gidanka da baiko na ƙonawa, zan cika wa'adodina gare ka, 14 waɗanda
leɓunana suka yi alƙawarin su, bakina kuma ya furta, sa'ad da nake cikin
wahala. 15 Zan kawo maka baiko na ƙonawa da dabbobi masu ƙiba da ƙamshin
raguna; zan miƙa bijjimai da awaki. 16 Ku zo ku saurara, dukkan ku dake
tsoron Allah, zan bayyana abin da ya yi domin raina. 17 Na yi kuka gare shi da
bakina, harshena kuma ya yabe shi. 18 Idan dana dubi zunubi a cikin zuciyata,
da Ubangiji bai saurare ni ba. 19 Amma da gaske Allah ya ji; ya kula da muryar
addu'ata. 20 Albarka ta tabbata ga Allah, wanda bai yi watsi da addu'ata ba ko
ya ɗauke alƙawarinsa mai aminci daga gare ni ba.

---

**Psalm 67**

1 May God be merciful to us and bless us
  and cause his face to shine on us Selah
2 so that your ways may be known on earth,
  your salvation among all nations.

3 Let the peoples praise you, God;
  let all the peoples praise you.
4 Oh, let the nations be glad and sing for joy,
  for you will judge the peoples with justice
  and govern the nations on earth. Selah
5 Let the peoples praise you, God;
  let all the peoples praise you.

6 The earth has yielded its produce
  and God, our God, has blessed us.
7 God has blessed us,
  and all the ends of the earth honor him.

---

**Zabura 67**

1 Bari Allah ya yi mana jinƙai, yasa fuskarsa ta haskaka wajenmu. Selah 2
domin a san hanyoyinka a duniya, cetonka kuma cikin al'ummai dukka. 3 Bari
mutane su yabi Allah, dukkan mutane su yabe ka. 4 Oh, bari al'ummai suyi
murna su raira domin farinciki, gama za ka hukunta mutane cikin adalci, ka
shugabanci mutanen duniya. Selah 5 Bari mutane su yabe ka Allah, bari
dukkan mutane su yabe ka. 6 Ƙasa ta ba da amfaninta kuma Allah, Allahnmu ya
albarkace mu. 7 Allah ya albarkace mu kuma dukkan ƙarshen duniya na
darjanta shi.

---

 generated on Thu Dec 14 18:53:07 2023

**Psalm 68**

**1** Let God arise; let his enemies be scattered;
let those also who hate him flee before him.
**2** As smoke is driven away, so drive them away;
as wax melts before the fire,
so let the wicked perish in the presence of God.
**3** But let the righteous be glad;
let them rejoice before God;
may they rejoice with gladness.

**4** Sing to God! Sing praises to his name!
Praise the one who rides through the plains of the Jordan River valley!
Yah is his name! Rejoice before him! [1]
**5** A Father of the fatherless, a judge of the widows,
is God in the holy place where he lives.
**6** God puts the lonely into families;
he brings out the prisoners with singing;
but the rebellious live in a parched land.

**7** God, when you went out before your people,
when you marched through the wilderness, Selah
**8** the earth trembled;
the heavens also dropped rain in God's presence,
in the presence of God when he came to Sinai, in the presence of God, the God of Israel.
